[YARDA.

1

Zaune suke cikin cikin ajin nasu,Su kadaine azaune sabida anfita break adaidai lokacin.
Kuma janyemata hannu tayi akaro na uku kamin tace" Zahra yakamata kidaina wannan tagumin ki gayamin matsalarki,Kindaisan duk fadin makarantarnan babu Wanda nake kulawa saike bansan damuwarki sabida Allah yagani NA YARDA dake to damme ke bazaki saki jiki daniba?Ko kina tunanin har yanzu bankai matsayin da zansan damuwarki bane?

"Ajiyar zuciya ta sauke me k'arfi kamin ta kamo hannuwan me maganar ta farko" Wallahi ba haka bane Jidda kema kinsan NA YARDA dake kilama fiye da yanda kika daukeni amma matsalata ta cikin gidace nakuma rasa ta yanda zan bulloma damuwar saidai inaso ki tayani da addua Dan Allah idan Allah ya kaimu wani lokaci zan gayamiki komai ammadai yanzu kifara tayani da addua tukunna kinji?

"Kwace hannuwanta tayi tana hararar zahra din kamin tace dalla ni kyaleni indai bazaki gayamin matsalarkiba to wallahi babu ruwana dake.

" Murmushi tasaki tana kuma kamo hannuwan jidda din kamin tace"yi hakuri sahiba Dan Allah wallahi dama matsalar dady ce yana cikin takura sannan muma muna buk'atar wadda zata dinga kula damu amma yakiyin aure,Jiya naji abokinshi yanamishi fada akan ya daina yima kanshi allurar kashe sha'awa tun kamin ta cutar dashi Amma nasan bazai dainaba hajiya kaka ma kullun saitamishi fada Amma yaki ji,Shine sai indingajin hankalina yanatashi wlh.

"Eh gaskiya akwai damuwa zahra amma ni sai inga kisameshi kimishi magana mana idan kika nunamishi kinaso yayi aure ai kila yayi nasandai damuwarshi bazata wuce kadda ya auro wadda zata cutar dakuba danhaka ke zaki nunamishi abinda kukeso tunda yanasonku kuma yanajin maganarki ko?
Murmushin jin dadi tasaki kamin tace eh hakan yayi nagode sosai wlh insha Allah yau dinnan zanyimishi magana komekenan zuwa gobe idan munzo makaranta sainaimiki bayani nagode jidda.

Yarane kusan sa'annin juna wanda shekarunsu bazasu wuce 15-16 ba sabida jidda ta Dan dara ita zahra din dakusan shekara daya amma kuma Kansu daya.
K'awancene tun farkon fara karatunsu Wanda har iyayensu sun san da zaman amintarsu.

Tsaye suke aharabar makarantar lokacin anata zuwa daukar yaran wasu amotoci wasu

amashina,Sukuma suna tsaye har lokacin agefe duk da cewa tuni direban dake daukar jidda yazo amma dayake yasaba ko'ajikinshi hasalima yana zaune cikin mota yanashan rake,Dan yasan indai ba mezuwa daukar su zahran yazoba to jiddan bazata yadda tabishi konan da can ba.

" Zahra Dan Allah ki yima yarinyarnan kitso cikin satinnan kalli yanda kitson duk ya zanzare Allah da wuya idan ba k'azanta zakiyiba zuwa nan gaba.

Wani uban tsaki zahran taja kamin tace amma kin rainani jidda,Wallahi haka kan Mimi yake duka yaushe dady yaimata wannan din nifa dama kinsan ban iyaba shiko ya iya tunda yanama momee kamin ta rasa nima bejima da dainaminba sabida beso muje ko ina wannan inyamurar ke zuwa tanamin saiya biyata,Itako Mimi kukan tsiya shiyasa yace inbari kawai ya dinga mata amma zan tsefemata anjima tunda babu islamiyya.

Da gudu Sadiq da faruk suka shige cikin motar bayan kowa ya mannama dadyn nasu Sumba akunci yayinda Mimi ta saka ihun kuka sabida sunrigata zuwa wajan dady din.

Dole yafito daga motar yana dariya tare da daukarta duk zata iya kaiwa shekara biyar amma tsabar gata yasa saikai tunanin bata wuce shekara biyu zuwa ukuba.

Gaidashi mukai tare nida zahra sannan ya wuce yasata gaban motar domin dama nan dinne wajan zamanta,Sallama mukai sannan nima na wuce wajan Wanda yazo daukata.

So daya ya kalleta ta madubi yaga Sam yau bata da walwala danhaka shima saiyaji hankalinshi yatashi,Shifa behada yaranshi da komaiba na duniya.

Kasancewar yau alhamis babu islamiyya shiyasa abincin safe kawai suka girka kamin sutafi danhaka yanzu data huta zatafara Neman abinda zatayimusu kamar yadda tai dadyn ya horata akai.

Saidai yau damuwardatake ciki saita saukar mata da kasala Allah yasama tai sallah amakarantar danhaka kawai saita haye gado bayan ta kwabe kayan jikinta.

Mimi tashigo dakin da kukanta tana shafa cikinta da alama dai kuka n yunwa takeyi.

Harararta tayi kamin tace"To sarkin fitina ai mundawo gidan yanzu zaki hana uban kowa kwanciyar hankali me akaimiki kike kuka?

Hawayenta ta share kamin tace yayanmu Abinci zanci ni bansan tea.

Harararta tayi kamin tace wuce bani wuri yau banda Lafiya sai zuwa anjima zanyi girki duk uban ciye-ciyen da kikayi dazu amma yanzu Dan kar mutun ya zauna Lafiya zakice yunwa wuce tai wajan dady.

Hannunta ya rike suka nufi falo domin dama yana tsaye kofar dakin yana sauraren mesukeyi,Da kanshi ya shiryamusu indomie danshima yunwar yakeji.

Saida yaga yaran sun natsu sannan ya yakoma ya jingina da kujera tare da lumshe manyan idanunshi wata irin kewar matarshice ta dabaibaye zuciyarshi jiyake kamar yasaka kuka

kozaisami sukunin zuciya.
Tashi yai ya nufi dakin zahra Dan beso damuwa tai tasiri cikin zuciyarta da gangar jikinta.

Gabadaya ya rungumota jikinshi yanajin zuciyarshi na tsananta bugawa,Bubbuga bayanta yafara kamin yafara magana ahankali cike da lallashi"Bansan damuwa zahra kinfi kowa sanin hakan shiyasa nabaki dama akan komai Wanda yashige miki duhu gayamin menene ya canzaki?

Rungumeshi tayi tana kuka"Dady mungaji da ganinka hakanan Dan Allah kayo aure musami wacce zata dinga debemana kewar mahaifiyarmu bazai yiwu ace koda yaushe Kaine komai dinmu ba kaima kana bukatar hutu kamar kowane mahaifi.
"Karki damu inshaAllah zanyi matsalar banso in dauko wadda zata zamemana matsala danhaka ki kwantar da hankalinki zanyi aure amma ba yanzu ba idan kuma kinada wacce ta kwantamiki arai to nabaki zabi Zahra.

Maman khadija

NA maman khadija.
Page 2

Tajima cikin halin tunani bayan barinshi cikin d'akin saidai tuni zuciyarta tafara kawo Mata wani kyakykyawan tunani,Wani mayen murmushi tasaki tare DA sakin k'aramin ihu murna fal cikin ranta lallai kakusa angwancewa my dady.

Duk da yanajin kamar zai iyayin danasani saidai ya Hana tunanin hakan tasiri cikin zuciyarshi musamman idan yai tunanin cewa yo wa zahra tasani balle hartayi abotar da zata iya bashi YARDA irin wannan shi bumma saiya bashi dariya danhaka tuni ya saki wani lafiyayyen murmushi saman kyakykyawar fuskarshi kai dady fa badai kyau ba.

Bayan nakoma gida wanka kawai nayi bataredana nemi abinciba danni abinci bawani damuna yayiba musamman idannacika cikina da cibanza ci wofi amakaranta,Kwasar littattafaina nayi na nufi falo jin muryar Yayana Usman dan shine ke kuma koyamin dukkan

abinda akaimana amakaranta matukar yana gida.

Kayan dayagama cin abincinakwashe nakai madafa sannan nadawo kusa dashi na lafe Dan Allah yayoni dason jikin masifa.

Janyeni yayi daga jikinshi yana hararata"To mage sarkinson jiki waike bakisan kibar mutun ya hutabane? Indai baki tashi daga jikinaba Allah kwallo zantafi yanzu inbarki.

Bakina na turo gaba tare da d'an dagamishi jiki kamin in koma dannariga nasaba rayuwa dashi.

"Haba Usman waikai Dan Allah meyasa kacika mitar masifane sabida Allah yarinyar nan idanbata rabekaba wa kakeso taje ta raba?Nifa bansan kana takurata da shegiyar mitarka ta gado,Kakarmu hajiya hauwa itace tai wannan maganar tanayi tana watsa hannu Dan ita Sam bata yarda kowaya tabaniba.

Be kulataba dan yasan kadantake jira yanzu ta taramishi mutanen dake kofar gida indai akan jidda ne

Ina kwance ajikinshi yaimin k'arin bayaninduk karatunan sannan yatashi zai fice,Rikeshi nayi ina kyafula manyan idanuna alamar kuka zan sakarmishi.

Waigawa yayi yaga gabadaya hankalin hajiya yana kan labaru datake kallo danhaka saiya koma ya zauna tare da zaunar Dani gefenshi gayamin menene kinji sweet sis?

Cikin yanayin muryatadatake me sanyi ga shagwaba nace pls Yayana kaje Dani Dan Allah.

Dama yasan fitinar bata wuce ta hakan danhaka saiya rungumeni jikinshi cikin muryar wayau yace yanzu zanje indawo bawani jimawa zanyiba zantaho miki da ice cream me shegen dadi kinji ko

Samu yai ya fice yanajin dadi cikin zuciyarshi godiya yake kumayima Allah dayasa berasa kanwarshiba kamar yadda ya rasa iyayenshiba.

Washe gari.

Can muka hade da zahra wadda yau naganta fayau da ita cikin farinciki sabanin jiya da take cikin damuwa da rashin walwala.

Rungume juna mukayi da ita kamar yadda muka Saba sannan sukuma suka gaidani.

Saida akaimana break kowa Yakama gabanshi sannan nazaro kular da hajiya ta zubomin dambun nama mukafaraci bayan na dibarma kannen zahra kamar yadda nasaba.

"Uhum saiwani murmushi kikeyi har yanzu kinkicemin komai KO dady yasami matar ne?

Dan tsaki taja kamin tacemin kinjiki saikace wani Wanda yarasa mashinshini aidama shi dady akwai masu kaunarshi da yawa kawaidai yaki basu dama ne amma jiya munyi magana dashi kuma yabani wuk'a da nama Zan zabamishi matar aure kalar wacce ta dace dashi wadda nasanta nasan halinta sannan na YARDA da ita fiyema da yanda ita ta yarda Dani.

Murmushi kawai nayi kamin ince amma naji dadi Allah yasanya alkhairi kinga nima wataran saiki ganni nazo gidanku yini tunda akwai mace amma yanzu danace zanje sai hajiya tace a a wai sai dadynku yayi aure.

"Murmushi itama tasaki kamin tace ki kwantar da hankalinki har kwanama zakiyi,Am yau juma'a sonake in nufi wajan hajiyakaka muyi shawara kome kenan zan taboki cikin wayar hajiya kokuma inzo ranar asabar.

"To babu damuwa Allah ya kaimu Lafiya.

Anan hirar tamu ta tsaya har akatashi bamu tsaya jiraba yau Danni yayana Usman yazo daukata sukuma tuni dama dady na jiransu.

"Wannan k'awar taki daga gani itama sarkin rikicice kamar ke ko? Cewar dady,Wanda ke farimciki ganin walwalar yarannashi duka.

Dariya tayi sosai kamin tace"Kai dady babu wani rikici damukedashi itakam gatane yai Mata yawa amma kuma bame cutarwaba kasan bata da iyaye duk sun rasu saidai yayanta da kakarta hajiya saikuma sauran dangi kowa yana sonta sunajin tausayinta shiyasa take shagwaba Amma wallahi dady jidda tayi saima ka zauna da ita gashi ta iya girki kamar kamar me kowane iri shiyasa nake kaunarta har cikin raina.

"Kuma dady tanasonmu sosai kullun saitabamu abinda dadi dama zata dawo gidanmu,Cewar Mimi wadda ketajan jelar kitsonta.

Wani irin murmushine ya kwacema zahra din Wanda har saida dadyn ya kalleta.

*********

Da ciwon Mara na isa gida duk da saida muka biya ya Usman ya saimin magani Wanda tun cikin mota yabani nasha Amma tsabar sangarta da kuka nashiga gida.

Da sassarfa tafito zaninta ahannu tana salati da sallallami kamin ta Dora da to keda ubanwaye wani shegene yatabaki incimishi uwa? Hajiya kenan iyayen rikici shiyasa nima nake sonta wallahi bata hada soyayyata da komaiba.

Jikinta nashige ina shesshekar kuka kamin ince hajiya marata ke ciwofa.

Saida ta lissafa kwanakin wata taga daidaine sannan ta furta"Wayyo Allah na sannu wallahi na manta da yaune zuwan abun muje ki wanka saiki kwanta kihuta ai ki kwantar da hankalinki akwai hisabi tsakaninki da wannan ciwon.

K'annen mahaifina na tadda zaune afalon sunacin dambu Wanda hajiya tayi abunta da kanta dan itafa har yanzu jinta take garau,Gaidasu nayi sannan nawuce daki yayinda sukabini da albarka kamar yadda suka saba dan sosai suma suke nunamin kulawa.
YARDA.

Na maman khadija.

3

"Fatima bintu zahra 'yar gidan manzo,Me zaki gayaminne naga bakinki yanata motsi alamar lallai akwai wani bayani dai,Cewar hajiya kaka wadda take mahaifiya ga dady.
Murmushi tasaki sannan ta riko hannuwan farar tsohuwar wadda itama idanunta nakan zahra din domin tanason zahra sosai musamman da itama take takwara wajanta.

"Kaka alfarma nake nema wajanki dangirman Allah kadda kice bazaki iyaba domin dole kece karfin guiwata kinji kaka?

"Karki damu zahra indai har inada dama basaikin hadani da Allah ba insha Allahu bakida matsala Allah yasa alkhairice maganar.

Cikin yanayi nakuma marairaicewa domin aji tausayinta tafara magana"Kaka nasan kina iya bakin k'okarinki wajan ganin dady yayi aure tunkamin Mimi ma tai wayau saigashi beda ma alama har zuwa yanzu musamman Dana Lura ko maganar ma beso, Rannan naji abokinshi nayimishi fada akan zai halaka kanshi indai beyi aureba amma sainaji yana gayamishi shifa bazai yadda ya auro wacce zata watsamishi gidaba kinga kenan sabida mu yaki auren,Saidai awashegari naita fushi da damuwa har saida ya tsareni da tambaya shine nace aure mukeso yayi sabida muna buk'atar makwafin uwa sannan yara da yawa kamar yadda kowayasan burinshi kenan Tara yara da yawa,To shinefa yace yabani zabi inje in zabomishi duk wacce nake ganin tadace dashi sannan bazata cutar damuba,To Alfarmar da nake nemadai wajanki itace sonake ki shirya yanzu muje gidan wannan k'awartawa ki ganta idan har tayimiki saimu dawo mufara shirya yanda abubuwan zasu kasance duk da nasan cewa dakyar idan hajiyar zata yadda da shirinmu.

Fuskarta cike da farinciki take furta Alhmdulillah amma naji dadi sosai Allah ubangiji ya shigemana gaba insha Allah komai zaizo da sauki indai kin amince da ita Sannan kin YARDA da ita babu matsala saimudage da addua yanzu tashi muje mudawo anshi wayata kiramin babanki tahir ya kaimu dan inaga shine kawai beyin nisa ranar juma'a.

****　　　****

Wando da rigane jikina na fakistan masu laushi tuni sunbi jikina saidan siririn kllabinta Wanda na daure gashinadashi.
Wainar fulawa nakeyi hankalina kwance inayi Ina karanto suratul Maryam kamar yadda d'abi'ata take nayin karatu musamman idan aiki nakeyi.
Sallamar zahra nadingaji sama-sama saidai banyi tunanin itan bace musamman dayake dazu muka rabu kuma tace kila sai asabar zata shigo wajena tabani labari.

Wani uban tsalle na buga lokacinda na tabbatar itace,Nan muka rungume juna muna murna yayinda hajiya batabi ta kanmuba sai sannu da zuwa da takeyima kaka.
Cikin mutunci suka gaisa sannan nakawoma kaka lemo da ruwa itadai sai kallona takeyi suna hira da hajiya muko ai cikin dakina muka shige mukafara hira saikace ba Dazu muka rabu ba.

"Dallah dazufa da ciwon Mara nashigo gida wallahi damma saida ya usi ya siyomin magani.
Dariya tai kamin tace ah kice abun yazo niko wallahi idan zanyi banjin komai saidai kawai inji yanayina ya sauya kuma danaduba sai inganshi.

Saida mukasha hirarmu sannan muka koma falo lokacin tuni su hajiya anzama k'awaye duk da dama sunsan juna amma hirar tasu tayau tafi armashi.
Jikin hajiya na shige tare da lafewa Ina leken kaka wadda keta dan kallona irin asace dinnan.

Shatara ta arziki hajiya ta hadamusu mukai sallama cikin jin dadi bayan hajiya tagama jaddadama kaka cewa itamafa tana nan zuwa.

*****

Hummm Ammma gaskiya harkinsa jikina yai sanyi zahra banda abinki yaya dadynku zaiyi da wannan yarinyar danya jagal da ita inagama ai da kadan ta girmeki yo ai duk shiririta gidan naku zai zama KO?

"Haba hajiya ya zakice haka dan Allah wallahi jidda babu abinda bata iyaba,Bama wannan ba ku lokacinda akemuku auran ai ko kaimu girma bakuyi,Nidai yanzu kawai temakon da zakimin guda dayane Shine idan nagayama dady zabindanaimishi kawai ki jajirce sai anyi hakan nikuma insha Allah Zan shawo kan ita jidda din.

"Uhumm to shikenan Allah yashigemana gaba insha Allah Zan kokarta.

Alhamdulillah,Cewar zahra tana lumshe manyan idanunta.

YARDA.

Na maman khadija.

4

Ranar asabar kwance nake saman cinyar hajiya tana tsefemin kaina yayinda idanuna suke lumshe harwani sauke numfashi nakeyi,Dan wani irin barci ke neman yin awon gabadani duk da nasan ba lallai tabarni inyiba tunda yamma tayi.

"Inason kalar gashinki dan irin na mamanki ne lokuta da dama abbanki kan hanata yin kittso wai yafison gashin ahaka'Cewar hajiya.

Kuma muskutawa nayi ina murmushi,Dan ba k'aramin dadi nakejiba aduk lokacinda take bani labarin mahaifana.

"Uhumm ashedai Abbana dan soyayya ne shima inasonsu DA yawa hajiya nayi kewarsu.

Shafa kaina tayi tana hadiye wani kululu daya sakkomata kadda ki damu suna cikin kwanciyar hankali da farinciki kedai ki dage dayimusu addua kinji KO?.

"To hajiya.

*** *** ***

"Zahra ki tsefe kanki ai kitso yau kinji ko?

Turo bakinta tayi kamin tace dady tun jiya nakecema zamuyi magana amma ka shareni kumafa nasan kanasane.

"Zahra kemafa kin iya rikici hadda na banza gayamin meya faru?

Kuma matsawa tayi jikinshi yayinda kirjinta kewani irin matsanancin bugu,Dady dama akan maganar da mukayi dakaine Dan Allah kadda kace a a dady kadda ka juya baya hakanshine farincikinmu.

K'ureta yai da manyan idanunshi yana kallonta yayinda zuciyarshi tai wani irin bugawa,Shifa ganewa kowa beyiba Amma wallahi tsoron matan yakeji duk da yanacikin matsanancin buk'atar macen.

"Uhumm ina jinki 'yar gidan waye? Kuma Ina kikasanta da har kikai mata YARDAr da zata iya shigowa cikin rayuwarmu?

Wani irin numfashi ta sauke tana sadda kanta k'asa Dan sai lokacinne taji wani mugun shakka da zullumin yimai maganar,Dady, Dady jiddace wadda mukeso ta maye gurbin mamarma idan ka amince da hakan.

Shiru falon ya dauka nawani lokaci yayinda idanunshi ke kanta yana karantar duk wani motsinta.
"Uhumm zahra jidda da yawa cikin garinnan kimin bayaninta da inda take idan naga dacewar hakan sai inyi yanda kikeso ko

"Dady Jidda k'awata wadda muke karatu tare nasan ka santa ai?

Wata irin zazzafar dariya yasaki wadda tasa gabadaya yaran maido hankalinsu kanshi sunamai kallon mamaki domin dariya ba d'abi'arshi baceba komai zai faru bewuce murmushi. Yatsanshi yasa yana nuna zahran yana dariya saida yayi me isarshi sannan ya sarara,"Nagode zahra KO babu komai yau kinsani nishadi Wanda narasashi tun kamin rasuwar mamanku,Amma inaso kima daina wannan tunanin dama nasan da wuya idan ba shirme zakiyiminba inba hakaba daganace nabaki zabi zahra saikimin maganar wannan danyar yarinyar wadda ko zata girmeki da kadanne? To bama hakaba ni kodacan danake saurayi bantaba sha'awar auran k'aramar yarinyaba mamanki ahekararta sha Tara na aureta lokacin inada ashirin da biyu koda kike ganina haka zahra inada shekaru bawai yaro bane ni, Dan hakamudaina wannan maganar kedai kawai kitayani da addua idan inada rabon kumayin auren to Allah yabani ta gari wacce zatayi daidai da tsarina,Amma ke yanzuma ai abin aimuku dariyane ace mahaifinku ya auri k'ank'anuwar yarinya kamar wannan ko? Ya idasa maganar har lokacin yana dariya mara sauti.

Bakinta ta tunzura tare da tashi tabashi waje tuni idanunta sunfara zubar da hawaye Dan takaici.

Da kallo yabita fuskarshi cike da murmushi shi abunma mamaki da dariya yabashi kamarshi da auran sa'an diyanshi ai abun aimishi dariyane ma.
Ganin yaran natakallonshi har lokacin yasashi watsamusu hannu tare da d'agemusu gira.
Duk maida hankulansu sukai akan kallon da sukeyi amma bunu-bunu sun waigo su kalleshi dole yasashi tattare kayan da yake aiki dasu yatashi,Kuma har lokacin murmushin be gushe daga fuskarshiba.

K'okarin shigewa bedroom dinshi yakeyi saiga zahra tafito janye da akwati tana kuka.
Kirjinshi yaji yai wani irin bugawa Ashe da gaske take,Watsar da takardun hannunshi ya nufeta yana kwace akwatin hannunta,"Ke bansan hauka da rashin hankali gidan ubanwa zakije nifa bansan rashin hankali da Neman fitina Ina zaki?
YARDA.

5

Wani irin kuka tasaki me matukar k'arfi Wanda yakuma rudashi balle da sauran yaran suka nufosu ko wanne fuska akwabe alamar kukan zasu taya yayarsu.

Rungumeta yayi ajikinshi yanadan buga bayanta alamun lallashi zuciyarshi ta raunana Dan beyi tunanin da gaske takeba.

"Kinga ku koma d'aki  kidaina wannan kukan zanyi shawara da hajiya kome kenan saimuyi magana amma ni bansan wannan damuwar haba mana fatimana ko so kikeyi duk ki sakamu cikin damuwa?

"Girgiza kanta tayi tana kuma sharbe hawaye,Ammafa cikin zuciyarta cike take da farinciki tunda dai magana zataje wajan hajiya to kuma dama sungama tsara komai.

Tun shigarshi cikin d'akin zagaye kawai yakeyi tsabar damuwa da tashin hankalin dayake ciki,Yanason farin cikin yaranshi domin beda kamarsu saidai bejin zai iya biyemusu Dan wannan dalilin idan har auran sukeso tayi to gara ya nemi babbar mace ya aura hakan zaifimishi sauki akan auran wannan kwailar yarinyar me shagwabar tsiya.

Kayanshi ya canza tare da daukar key din motarshi yabar gidan dole ya sanarma hajiya da maganar nan tunkamin abun yai nisa har rayuka su baci, gara idan fada zaikai zahra din aimata to da sauki akan hakan.

***

Zaune muke muna hira nida hajiya sa ya Usman Wanda lokuta da dama nake kiranshi da ya usi,Hankalina kwance NA kalleshi jiya kanacan yawonka zahra tazo da kakarsu hajiya kuma sunjima wlh.

"Mirmushi yayi yana shafar suman kanshi tare da kallon hajiya,Aiko bansan zasuzoba Dana tsaya mun gaisa inafatan kinadan shigar dani wajanta Dan gaskiya nida gaske nake indai sunshirya.

Hajiya dake rike da haba takama dariya"Lallai yau naga yayan banza kai bazaka iya kai kankaba sai k'anwarka zata tura aiko indai hakane inaga baka da rabo cikin jikinta.

"Kai hajiya"Kai hajiya Dan Allah yanzu idan bakinki beda kyau ai shikenan kin kasheni kinyimin baki haba mana,Wallahi Ina sonta da gaske,Kinga auta tashi ki shirya mukai musu ziyara ma.

Da gudu na shige dakina na shirya cikin atanfa Riga da siket bawata kwalliya nayiba amma fuskata fes take Dan sosai nakeda baiwar kyau.

Wani irin k'amshi nakeyi me kwantar da hankali Dan nifa akwaini dason k'amshi koda yake gadanayi wajan hajiya nima

Gefenshi na zauna Ina cewa to yanzu gidansu zamuje ko gidan hajiyarsu sabida ba lallai ataddasu waje dayaba balle yau asabar.

"Haba ai kamata yayi ace ko k'ananun waya akwai ahannunku domin ganin junankuma,amma muje gidan kakarsu din kawai idanma basunan saita kiramanasu amma zuwanmu gidansu akwai matsala tunda basu da mahaifiya.

*** ***

Zaune yake gabanta k'afafunshi atankwashe yana faman jiranta bayan yagama koramata bayanin duk abinda ke faruwa.

"Hummmm To ai Ni abinne ya dauremin Kai wallahi kuma wannan abun duk laifinkane babu yanda banyi dakaiba akan kanemi matar aure idan ma ba kaiba kodan yaranka amma alokacin sabida bakason maganar saima ka dauke k'afa da zuwa gidannan saida na nemeka nariga nagamaka yaranka na buk'tar matar da zata zama uwa agaresu tunda kai biris da maganar aigashinan yanzu diyarka taimaka zabi ko?

"Umma Dan Allah kice wani Abu nidai kiyi hakuri sabida Allah Ina zankai sa'ar diyata? Bama wannanba wayasan kalar haukan da zasu dingayi cikin gidan bannan Dan wallahi wannan yarinyar tafisu rikici Dan gata yaimata yawa.

"Uhumm yanzudai kasa direbanka ya kawomin su zahra din kaikuma ka kiramin yayanku yazo kawai aje gidansu ayi tambaya danni hakan yayimin daidai dama duk Wanda beji bariba ai saiyaji woho.

"Kuma marairaicewa yayi yanajin yanakuma shiga wani mugun tashin hankali,Idanunshi ya zubama hajiyar yanajin kamar ya Dora hannu aka yaita sakin ihu kozaisami sukuni.

Wayarshi yasa yakira habu Direba sannan ya kira yayanshi din kamar yadda hajiyar ta buk'ata sannan yakoma gefe ya makure saikace almajirin daya rasa abinci.

Suna nan zaune zaman shiru lokaci zuwa lokaci hajiyar NA kallon yaron nata tausayinshi takeji sosai,Saidai tanaso yasami nutsuwa shima kamar sauran magidanta tunda yasami shaida kudi basu rudeshiba yafara harkar banza dukda yanada damar hakan saidai gara adauki mataki tunkamin abun yazo yafi karfinshi,Dan sha'awa mugun abuce.

Sallamar Alhaji musa tasa dadyn kuma tunzuro baki kamar k'aramin yaro danshima dadyn autane Amma ahaka har yakema wani sherin shagwaba.

Dariya Alhajin yayi kamin yace"hajiya meya farune naga autanki nata kumburi kamar fanke

yaji yis

Dariya tayi sosai kamin tace kaimadai ka fadi waifa ahaka wata yakema sharrin tacika shagwaba alhalin gatashinan alike yana fama da ita,Diyarshice ta nemomishi matar aure shine yazonan zaimin rikicinshi.

Gama bayaninta ga Alhaji musa saiga su zahra sun dira gidan,Nanfa Falon ya dauki wani shiru na musamman.

Sallamar mu cikin falon takusa dauke numfashin dady Wanda dama yake cike da fargaba musamman ganin har lokacin zahra bata da walwala.

YARDA.

NA maman khadija.

6

D"aure fuskarshi yayi tamau irin karma arainashi dinnan,Ammafa saiya samu kanshi da kasa dauke idanunshi daga gareni so yake yaga wata alama dazatasa aga dacewar aurena dashi.

Tsallen zahra da ihun su faruk yasaka hankalin kowa komawa kanmu rungumeni sukayi muna murna,Akunyace ya usi ya gaidasu sannan nima na gaidasu muka wuce cikin bedroom din hajiya kaka.

Tsam yatashi kamin yace hajiya bari injirata waje kamin sugama gaisawa dama wucewa zamuyi nace bari inbiyo mu gaisa ashema su zahran na nan?

"Eh fa amma aidakayi zamanka usmanu ai anriga anzama daya ko?

"Babu komai hajiya bari injirata waje.

Ajiyar zuciya dadyn ya sauke me k'arfi tare da maida hankalinshi kan hajiyar ya kafeta da idanunshi jiyake duk ya muzanta.

"Dariya tayi kamin tace"dady me amarya lallai zakasha amarci.

Dariya alhaji musa yayi shima kamin yace"To kai Habib menene na damuwa akan wannan lamari tunda sunaso kawai zamutayaka da addua amemakon kaje ka dauko babbar mace wadda zata wahal dakai da yaranka ko?

"Uhumm nima abinda nake nunamishi kenan to Amma kasan habibu da shegiyar kafiyar tsiya.

"Yanzudai kaje ka kwantar da hankalinka saimusan abinda za ayi kaga tunda har makarantarsu dayama ai abun zaizo da sauki kaima zakasami nutsuwa tunda yarinyace amma auran babba bazaimakaba ayanzu,cewar Alhaji musa.

"Fuuuu yatashi yabar gidan yana sauke numfashi Dan sosai yaji ranshi yabaci musamman dayakejin sautin su zahra din sunata shewa jiyake kamar ma dashi suke.

Da kallo suka bishi lokacin dayabar gidan,Kamin hajiya ta dora da cewa"Uhum kyale sakarai nan gaba kadan zakaga yafara jin dadi harma fatarshi ta canza tunani yakeyi sai babbar macece zata iya kulawa dashi sabida shirme,Yanzu kaje ku shigemai gaba komeyakamata kuyi kuyishi Dan Allah inafatan Allah ya doramu akansu su amince mana da auran ayanzu domin ba lallaibane su yardaba indai ba itace ta nuna tanasan hakanba.

*** ***

"Kai kuje falo zamuyi magana idan mukagama saiku dawo,Cewar zahra tana harararsu Mimi da suka cika dakin da hayaniya kowa k'okarin bawa jidda labariyakeyi.

"Harararta nayi nace saikimin bayanin abinda yasa kika korarmin k'anne.

Dariya tayi kamin tafara magana cikin yanayi aji tausayinka,Jidda kinsan Ina sonki Ina kaunar zama tare dake sannan na YARDA dake Dan Allah ki temakamin kamar yadda Allah yabaki ikon iya temakon Dan Allah ki amincemin da wannan bukatar tawa kinji?

Haka kawai naji jikina yai sanyi tare dajin faduwar gaba,Amma hakan be hanani riko hannuwantaba"Karki damu zahra munriga munzama daya kawai ki gayamin meyafaru?

"Uhumm ba fadinba jidda Alkawari nakeso kimin.

"Murmushi nayi kamin ince karki damu naimiki Alkawari insha Allah duk abinda kikeso indai har inada dama babu abinda zai gagara.

"Hannuwana takuma matsewa cikin nata kamin tace nagode jidda Allah yasakamiki da alkhairi,Dama Alfarmar danake nema wajanki shine inaso ki amince ki auri dadynmu kidawo gidanmu da zama.

"Atsorace na fisge hannuwana daga cikin nata tare da zubamata manyan idanuna,Kirjina kamar zai fashe tsabar fargaba da tashin hankali"Dakyar nacemata Anya kinada hankali kuwa zahra nice Zan auri dadyn?

"Temakamana zakiyi jidda dan Allah ki tausaymana bamusan kalar wacce zai daukoba Dan Allah.
YARDA.

NA maman khadija.

7

Wani kallon banza nabita dashi kamin in mike tsaye,Bazan iyaba zahra bazan iya auran dady ba keni babuma tsarin aure ayanzu cikin rayuwata duka nawa nake? Sannan saikice in auri dady? Shi kanshi yace ya Auri wa?

To bama wannan ba idan har kikai tunanin sabida inasonki ne kuma na YARDA dake zakimin wannan abun to kisani ni bazan iya wannan cin amanarba baban k'awata wadda NA amince da ita na YARDA da itane Zan aura? Kai Ina badaniba wallahi danhaka kinga tafiyata,Dama ya usi ne ya matsamin in rakoshi tunda kinsan sonki yake amma wallahi indanasan wannan maganar Zan tadda da baki ganniba zahra.

Kwace jikina nayi NA raba ta gefenta Zan wuce saidai hakan ya gagara dankuwa hajiya kaka na tsaye ta tare kofar da Alama tajima wajan tsaye.

Kukan zahra ya cika d'akin wani irin kuka takeyi me matukar taba zuciya da sauti me k'arfi Wanda hakan yajawo hankalin kannenta dake falo shigowa kamin wani lokaci suncika d'akin da kuka.

Nima gefe na durkushe tare da fashewa da kuka yo ai abinne daban mamaki tare da rikirtawa yo yaushema hajiyata zata yadda da wannan maganar.

Saida sautin kukan kowa yafara k'asa sannan hajiya kaka tafara magana cikin hali na alhini dakuma Tausayi"Inaso ku saurareni kuji abinda zance domin wannan koke-koken babu abinda zai harfar muku sai k'arin damuwa danhaka ku kwantar sa hankalinku duk ku saurareni.

"Ke Jidda dake Zan fara da farko inaso inbaki hakuri akan wannan maganar sannan kuma inaso ki fahimci inda wannan maganar ta dosa dangirman Allah Ina rokinki Dan soyayyar da kikeyima iyayenki kiyimusu wannan alfarmar  jidda,Kinsan dai yanda wannan zamanin yake acakude kuma ahargitse Wanda mutane da yawa babu abinda sukasagaba sai hassada da bakinciki sannan uwa uba mugunta kusan kowa kanshi yasani ko dukiyace da mutun yafison yacita dagashi sai yaranshi,Mata sunason  me kudi komai mugun halinshi yayinda maza keson Mata kyawawa koda basu da tarbiyya,Kinga kenan kotawane bangare akwai matsala KO?

"To hakanne yake kasancewa ga maza wa inda suka rasa matansu,Daga lokacinda namiji ya rasa matarshi tafarko ma'ana uwar 'ya'yanshi shikenan saiya kasance cikin zullumi da tashin hankali sabida tunanin yanzu da wacce zai zauna sannan zata soshi tsakani da Allah kuma ta kula da wa innan yara nashi?

Tabbas wannan abun damuwane da tashin hankali to wannan k'addararce ta fada akan habibu yanason matarshi  Jidda so irin na kwantance saidai lokacinda sukafara Tara iyali kawai sai Allah ya dauke rayuwarta,Shikenanfa saiyashiga cikin garari damuwa da tashin hankali,Wannan daliinne yasa babu kalar matsawar da bamuyimishiba akan yai aure tun Mimi na jaririya amma ya kiya sabida beyarda da kowaba akan yaranshi gani yake kowa zai iya cutarsu,Dan Allah kinga laifinshi jidda?

Yana bukatar kulawa amatsayinshi ta cikakken me gida amma yarasa kuma sabida farincikin yaranshi ya hakura,Wanda ahalin yanzu Allah ne yasakama diyarshi hankali da

nutsuwar tunanin yakamata yai auren data matsamishi shine yace yabata zabi,Itakuma taga babu wacce ta dace da wannan matsayin kamar ke,Dan Allah jidda ki amince da hakan kizama cikin family Dina hakan zaisani farinciki,Bazai hanaki karatunkiba kinga gaki ga k'awarki kuje makaranta tare kuyi girki tare Ku gyara gida tare sannan Ku kula da kannenku,Idanma bazaku iya aikinba Zan nemi dattijuwa wadda zata dinga yimuku sauran ayyuka kinji?

Tsawon lokaci d'akin yai shiru sai sheshshekar kukana Dana zahra dake tashi lokaci zuwa lokaci.

"Mikewa nayi tare da rabawa ta gefensu na fice daga gidan yayinda zahra tabini da sauri saidai tuni nakusa shigewa mota ma.

Batadamu da kayan dake jikintaba ta dawo gabana tana kuka"Dan Allah jidda ki amince kinji kadda kitafi bakice komaiba!!!

Idanu ya zaubamana yana mamakin meyakawo wannan tashin hankalin haka alhalin yaga yanda muka cika da farincikin ganin juna da farko? Rungumeni yayi jikinshi kamin ya kalleta"Sorry kije gida zakuyi waya anjima.

Tana nan tsaye har saida muka bulle Dan Ina hangen lokacinda hajiya kaka tafito tashiga da ita gida.

Ajiyar zuciya na sauke me karfi tare da lumshe idanuna,Allah yasani inason zahra sabida inajinta cikin jikina sosai da sosai na YARDA da ita tokuma damme zatace inwani auri dadynta,Duk da ba tsoho bane amma ai yaimin girma,Kumama nasan hajiya bazataimin aure yanzuba.

Lamo nai cikin motar idanuna arufe tuni tunani yagama dabaibayemin zuciya,Shidai ya usi tukinshi kawai yakeyi amma na Lura hankalinshi na kaina.

*****    *****

Lamo yayi Saman makeken gadonshi tsabar tunani sai mutun ya zata barci yakeyi Amma Ina,Damuwace kawai ta saukarmishi da wata muguwar kasala da ciwon kai.

Wayarshi dage ring ya jawo idanunshi arufe ya Kara wayar akunnenshi,"Shigo ciki kawai sulaiman Ina ciki,Abinda yace kenan ya ajiye wayar.

"Kai man yana ganka kwance nan jikin ko garin? Abokin ya idasa maganarshi tare da zama gefen gadon.

"Uhumm kaidai bari kawai sulaiman zahra ke Neman samin hawan jini wallahi.

Idanunshi waje yake kallonshi"Kamin yace banganeba kamar yaya?

"Ta matsa sainayi aure sulaiman data isheni sainai tunanin inyimata dibara kawai,Sainace

nabata zabi ta zabomin wadda ta YARDA da ita,Wai kawai saigata da maganar wata yarinya kuma wai abin haushi hajiya tahau kan maganar ta zauna.

"Hummm harkabani tsoro wallahi to inaga wannan aiba abun damuwa bane Habib kana cikin buk'atar aure koba komai kaima zaka sauke abinda ke damunka sannan kaga akwai shakuwa tsakaninsu insha Allah bazasusha wahalar zama da itaba,Akan na nemo wadda zata tagayyarasu inace kaima abinda kakejima tsoro kenan KO?

"Baka ganeba sulaima yarinyarnan fa muguwar kwailace sa'an ita zahra dincefa sabida Allah idan ba shiriritaba mezan gani cikinsu babu me hankalin kirki,Sannan wannan yarinyar KO rabin larurata bazata iya daukaba balle Dan yarinyace sosai.

"Kajika da wata magana Dan Allah kaidai kawai ka kwantar da ha kalinka kayi addua amma wannan duk bawata damuwabace indai takai zahra zata iya daukarka tunda Ina tuna zatakai irin 15-16 haka kuma kaga kamin Ku sabama takuma wayau,Sannan kadda ka manta auran k'aramar yarinya wallahi shine kwanciyar hankalinka domin babu yanda za ayi ka dauko mace me budadden ido me shekaru kace wai zata kulamaka da yara,Kaima kasani KO?

Kasa motsin kirki yayi saidai yabi abokin da idanunshi gabadaya kanshi ya kulle,Tsabar tunanin ko rakiya besami sukunin yima abokin nashiba danshi sauri yakeyi zai dauko matarshi daga gidan kunshi.

***        ****     ***

"Ki kwantar da hankalinki zahra insha Allah zata amince aikinga tanada tausayi nasan zata amince abunne yanzu zatajishi Asama,Yanzu saimu dage da addua muzubama sarautar Allah ido, Danshima wannan rigimammen uban naku sai anyi da gaske indai anaso yayi yanda akeso,Gobe idan Allah ya kaimu saimuje gidan nasu,Da kaina zanyima ita hajiyar bayani nasan zata fahimta kinji ko?bansan wannan kukan naki kalli yanda duk kikasa kannenki cikin damuwa!!!Cewar hajiya kaka datagama lallashin zahra

YARDA.

Na maman Khadija.

8

Wani irin sukuku haka na idasa yammacina yayinda hajiya tai tambayar duniyar nan amma nai biris da ita dole ta zubamin ido tanajiran ingama kuncin sannan Ingayamata abinda ya faru.

Abangaren ya usi shima duk saiyaji babu dadi musamman dayana tsaye awaje lokacin da dady yafita kuma da alama afusace yake shima,Fatan alkhairi kawai yabimu dashi kamin yace idan tayi wari ai dole muji.

Washe gari haka na shirya na nufi makaranta tuni na washe saikace banice na kwanta da mugun kunciba,To gaskiya dama ni haka nake yanzu zaka batamin arai amma kamin wani lokaci na huce,Allah beyoni da rikoba.

Kasancewar narigasu zahra zuwa sainaji duk babu dadi sabida bafa k'aramin sabone tsakaninmuba.

Sai lokacinda zamu shiga aji sannan suka iso shaf na manta da wata magana datashiga tskaninmu jiya danhaka da sauri na nufesu Ina murmushi.

Manyan idanunshi ya bude gaba daya ya zubaminsu wani irin kallone yake bina dashi daga sama har k'asa tunanin abinda zai diba yakeyi cikin jikina kawai yakeyi yayinda yakemin wannan kallon,Ajiyar zuciya ya sauke jin Mimi ta sakarmishi Sumba ta sallama.

Zahra ya kalla amma tuni ita ta isa wajena,Matsowa nayi jikin motar Ina riko hannun Mimi daketa mikomin hannunta in sakkota daga motar,Nace dady Ina kwana?

Yatsanshi yasa ya shafi girarshi kamin yace Lafiya lau ya hajiya?

Tare mukashige aji,Saidai jikina yai sanyi ganin yanda zahra bata da walwala sosai,KO magana dakyar takeyinta.

Bayan anyimana break ne na tsareta da tambayar meyafaru ko bata da Lafiya ne?

"Amma kin rainani jidda ingayamiki matsalata da damuwata kinada halin temakamin kiyi biris Dani shine yanzu har kinada damar tambayata KO banda Lafiya?Wallahi kinbani mamaki bantaba tunanin zakimin hakaba, Nai tunanin Acikin YARDAR da mukaima juna nidake babu wani Abu dazan nema gareki ki kasamin shi sai wannnan Wanda ni aganina bawani abun damuwabane kumafa nima Zan ramamiki tunda ya Usman na sona sai kawai in aureshi kinga dai muna tare KO?

"Dan murmushi nayi kamin ince eh fa hakane to na amince Amma zahra kina ganin dady bemin girmaba?

Dariyar farinciki ta saki kamin ta riko hannuwana,"Dallah bemiki girmaba ainasan rainonki zaiyi bawai maganar wani abuba,Nidai fatana ace dadyna yanada aure,Sannan yasami nutsuwar da ake buk'ata kinga nima da mun idasa makaranta kamin muwuce gaba sai kawai Adauramana aure daya usi ko?

Murmushi kawai nayi dan wani irin sanyi naji jikina yayi.

***

*****

Saida kowa ya natsa sannan alhaji musa yai bayani kamar yadda masu buk'atar neman aure kanyi.

Hannuwan hajiya akirji take binsu da kallo kamin tace"Ku dakata dan Allah wai wace jiddan ce ta turoku inace dai makuwa kukayi bawai jidda tawaba?

Alhaji shehu k'anin mahaifinsu dadyne ya muskuta tare da gyara zama kamin yace" Hajiya jidda taki dai muke nufi domin babu yanda za ayi muzo alhalin bamusamu kwarin guiwaba.

"Baba aminu Wanda tsoron Allah yasashi tagumin dole,Sai bin mutanen falon da kallo kawai yakeyi shine ya kalli, Ya Usman kai jeka makarantarsu jidda ka daukomin ita, kutaho yanzu dan Allah kaga anbar mutane zaune.

Cigaba da tattaunawa sukayi Akan maganar cike da mamaki bayan barinshi falon musamman hajiya wadda tsoro yagama kamata,Ganin yanda masu Neman auren suka jajirce.

Bak'aramar faduwar gaba najiba lokacinda malamin mu ke kirana saikuma danafito naga ya usi,Zahra ce ta rikemin hannu idanunta cike da kwallah"Kimin alk'awarin bazaki canza daga maganar da mukayiba jidda!

"Karki damu zahra nariga na amince bazaki sami matsalaba tunda kema zaki auri Yayana danhaka ki kwantar da hankalinki.

Murmushi tasaki kamin face saikin dawo amma dan Allah kadda kik'i dawowa.

Hannun ya usi na rike bayan munshiga cikin motar,Kasa hakuri yayi har saida yaimin magana,"jidda meke faruwane tsakaninki da zahra nifa nakasa fahimtar komai!!!

"ALLAH babu komai Yayana,Menene hajiya ke nemana?

"Watsa hannuwanshi yayi kamin yace nima bansaniba kila unguwa zakuje.

Jikin hajiya na rabe lokacinda naga idanun kowa akaina dakyar nasamu na iya gaidasu Sabida zullumi.

"Hajiya kijeda ita ki tambayeta,Cewar baba yusuf shima yayan mahaifinane.

Hannuna ta rik'a tai ciki dani yayinda falon yaiwani shiru na musamman,Kowa da abinda yake kissimawa cikin ranshi.

""Ke jidda dan gidanku gayamin su waye wa incan?
Turo bakina gaba nayi Zan sakamata kuka dan nima bansansuba"Kai hajiya ba yanzu na gansuba zaki tambayeni nima bansansuba to.

Rikeni tai cikin lallashi tace" Jidda kadda muyi haka dake ki gayamin meke faruwa wa incan zuwa sukai Neman aurenki fa.

Kauda kaina nayi daga kallonta kamin ince eh dadyn zahra Zan aura sabida itama zata auri ya usi kawai ki amince Zan dinga zuwa nan gidanki kokuma kikoma gidansu zahra din kema.

"Tirk'ashi lallai kuruci dangin hauka, Ke ubanwaye yabaki wannan shawarar lallai na yadda baki da hankali to badaniba wallahi danhaka Bari naje naci uwarsu tukunna tunda suma naga alamar Neman saitin kwakwalwa suke nema.

Fuuuu tatashi tabar falon batare data kuma kallonaba Niko ai KO ajikina dan bani da damuwa akan masifarta dannasan Ina matsawa na nace dole itama ta amince.

YARDA.

Na maman khadija.

9

Wani birki taja tana sauke numfashi dan hajiya akwaita da zafi wani lokacin musamman idan taboni akayi.
"Kunga kadda muyi haka daku dukanmu nan munsan cewa Jidda bata da hankali balle wayau danhaka kutashi kutafi bakinku alekum Dan nidai banga haukan da zaisani amincewa inbada auran Jidda ayanzu ba,Danhaka kuyi hakuri ya nemi wata Dan Allah.

Malam Nura Wanda duk yafisu tsufa shine yafara magana cikin kwantar da Kai musamman daya Lura itafa hajiyar atsaye take"Kinga zauna hajiya ai maganar duk me saukice insha Allah babu wata matsala Dan alkhairine ya kawomu,Yarinya dai ta amince domin itacema ta bashi iznin turowa ga iyayenta sannan bafa tauyeta zaiyiba zatacigaba da karatunta har zuwa lokacinda zatace tagaji Dan kanta sannan shima bazai matsamata da amsarshi amatsayin mijiba zai jira har zuwa lokacinda zatakuma girma shidai fatanshi damu baki daya Ku amince ayi hidimar nan kodan YARDAr dake tsakanin yarannan domin dama YARDAr ce ta kasance sila.

Kasa magana tayi ayanzu sabida takaicin sunki fahimtar ta danhaka saitai shiru saidai tabisu da kallo.
Baba Ibrahim Wanda shine babba cikin yaran hajiyar shine yafara magana cikin

nutsuwa"Munji buk'atarku amma munaso kubamu lokaci muyi shawara sannan saimu tuntubeku insha Allah ba matsala.

Nan sukaita godiya kamin suyi sallama subar gidan cike da fatan nasara akan hidimar.

Wani irin shiru falon ya dauka bayan dawowarsu daga rakiyar bakin.

"Uhumm hajiya kinyi shiru bakice komaiba,Cewar Alhaji Yusuf k'anin mahaifina.
"Uhumm toni yanzu mezancemuku wallahi abun ya dauremin Kai,itafa da gaske takeyi auren takeso,Kumama sabida Allah duka jiddan nawa take? Da zata fadama wannan babban kusan sa'an babanta iye?
Danhaka kai Usman kiratanan tazo kila idan taga idanun iyayenta maza ta janye.

Makurewa nayi cikin kujera Ina zare ido musamman danaga gabadayansu ni suke kallo balle ya usi harwani kalar tausayi yakoma damuka hada ido.

Baba Ibrahim ne ya yafitoni da hannunshi tare da cewa "Zonan me sunan manya dawo kusa dani in tambayeki kinji KO?
Matsowa nayi jikinshi batare Dana kalli idanunshiba sabida tsoron ko fada zaimin,Hannuwana ya Kama ya rike sannan yace"Wai kece kika turo wa incan mutanen Neman auranki?
Hannuna daya rike naketa mutsu-mutsun kwacewa amma ya rikeshi kam,Dole na daga kaina ahaka,Alamar amsawa.
"Tirkashi,Cewar hajiya tana rike da baki.

Kuma sassauta murya yayi alamun lallashi"Mesunan hajiya auren kikeso yanzu kodai abasu hakuri saikin kuma girma?

Sabodayi"danhaka bansan lokacinda na turo bakina gaba ba Ina fadin nidai a a baba yanzu nakeso,Zan zauna dasu zahra zamuje school tare hadda islamiyya kumama ai itama zata auri ya usi.

Baki hajiya ta bude zatai magana amma Baban ya hanata ta hanyar yimata alama datai shiru,"To shikenan Kai Usman tashi ka maidata makaranta.

Gaba daya hajiyar suka tausa akan tai hakuri kawai ayi abun,Aiko ranta besoba tuni tafara durama dady zagi akan zai rabata dani hadda hawayenta tsabar bahaka tasoba,Saidai tana tunanin kadda taje tahana kuma ni inshiga damuwa.
Danhaka anan suka tsaida magana nan da kwanaki biyu zasu nemi iyayen dady domin suzo atsaida magana saidai sunyi shawarar za a daura aurene kawai in tare sauran shagulgulan biki idan Allah yasa nayi candy Lafiya sai ahada gabadaya ayi.

***,,,     ***,,,

"Kasan wani Abu habibu Bari inyimaka yanda zaka gane dannaga kana Neman ka maisheni sakarya,Wallahi wallahi saika auri yarinyar nan kajima na rantse indai kaga ba'ayiba to ka tabbata iyayentane suka haka danhaka idanma zaka kwantar da hankalinka ayi komai cikin nutsuwa to inkuma shirme zakaitayi gaban yaranka to wannan damuwarkace ba tawaba nagayamaka,Fiiiiiiii tatashi tabar mishi falon bayan tagama zabgamishi harara kamar idanunta zasu fado k'asa.

Tashi yai yakoma saman kujera ya kwanta tare da lumshe idanunshi,Tariyo dukkan yanayin Jidda yakeyi,Saidai haryagama tunaninshi be hango wata makusa ajikintaba sai kuruciya da shagwaba to ahakan Ina zaikai wannan mitsitsiyar yarinyar Dan Allah?

Yana nan kwance besan lokacinda barci yai awon gaba dashiba.

**""""****"""

Ranar laraba,Abu kamar wasa saiga k'aramar magana tazama babba dankuwa iyayen dady basuyi k'asa aguiwaba aranar labara suka kuma dawowa inda iyayena suka amincemusu akan sun amince da wannan aure danhaka idan sun shirya ranar juma'a sai adaura aure intare ammafa akwai shagalin biki idan mungama makaranta.

Sunyi farinciki da murna inda tun anan suka zube komai na buk'ata sannan suka wuce,To dama abune na ansan juna ansan tushen juna balle atsaya wani kalkale kalkale.

Danhaka saimu hangi juma'a insha Allah.

YARDA.

Na maman khadija.

10

Ganin yanda taketa kallona yasani turo bakina gaba Ina harararta,Waike hajiya mene da zaki tasani kita kallo hadda tagumi KO mutuwa zanyi ne?

"Uhum to wama yasani ko mutuwar zakiyi ammadai nasan indai har kika kuskura wannan habibu yake da suna ko habibane oho dai matukar ya doramiki nauyinshi nasan saidai wata

amma ba keba.
Batare da wata damuwaba nace yo hajiya shi beda hankaline da zai doramin nauyinshi inama zai ganni balle ya danneni ai muna tare dasu zahra koda yaushe ko?

"Mitsww taja tsaki kamin tace wawuyar banza Ana rabata da kiwon akuya tana kyalla ta haihu,To danneki zaiyi ya amshi hakkinshi indai an daura auren.

"Hhhhhha Kai hajiya to meye idan ya amshi hakkin nima ai zai sauke nawa kinga zandingacin kayan dadi kamar ina wajanki zaikuma dinga biyamin kudin makaranta kinga shikenan kunhuta damin siye siye.

Tsamm tatashi tabar dakin tana sharar hawaye itafa duk Dan farincikina takeyin komai amma Sam naki ganewa tasandai kewata kawai saita kusa kasheta yanda tasaba Dani bata Saba da yaran data haifaba sannan tafi tausayina fiye da kowa da komai saigashi kwatsam Rana guda wani k'aton gardi zai rabamu,Bari akwana biyu itama cangidan zata koma idan taji takasa jurewa,Ragwas ta zauna akan kujera cikin falonta Wanda ke cike da 'yan biki wa inda suka kasance surukanta da 'ya'yanta Mata tunda gobene daurin auren,Dole ayi wasu abubuwan koda ba dukaba.
Tunanintane ya yanke lokacinda Gwaggo Uwani kecewa"Dan Allah hajiya ki cire wannan damuwar aranki wallahi kuruciyace kawai ke damunta amma idan ankwanabiyu zata fahimci abinda ake nufi da aure,Amma yanzu kinagani duk Wanda yaimata magana Neman yimishi kukama takeyi Dan Allah ki kwantar da hankalinki.

""******""""

"Zahra kinga abinda  kikajamin ko?Sabida Allah auran sa'arki!!!Gashinan kinsa hajiya tatashi hankalina ko?Idan ita Jidda din batasona shikenan kin hadani da wani aikin banda Wanda nakefama dashi ko?

"Kayi hakuri dady insha Allah zakaji dadin aurannan ni abinda yasa kaga na nace sai ita Wallahi tanada hankali sosai ga ilimi na addini dana boko tanada tarbiyya gatanda akaimata be lalatataba dady ita kadaice zata zauna damu tsakani da Allah ka duba su Mimi yanda suketa murna jin zata dawo gidanmu insha Allah bazakai Dana saniba dady saima godiya da zakamin,Kuma nasan Jidda zata soka aiba tsufa kayiba inbama Wanda yasaniba ai baza'ace Kaine ka haifemuba Dan Allah kayi hakuri dady kabamu goyon baya pls dady👏🏻.

"Shikenan zahra Allah yaimuku albarka yasa hakan yazama alkhairi garemu baki daya.

"Yeeee yauwa dadynmu mungode Allah yasa haihuwar farko Jidda tabamu twins masu Kama dakai dady.

Rungumeta yayi yana dariya shima saiyaji zuciyarshi tacika da farinciki musamman kwanakinnan da yakejinshi sai ahankali,Lallai zahra kin rainani wlh.

"Kije ki duba wancan dakin masu gyaran sungama saikiga idan akwai abinda ake buk'ata kinsan gobe zasu kawota tokuma bansan komai akantaba na kalar abinda takeso danhaka saiki duba ko?

"Eh hakan yayidady Allah ya Karo budi.

. Irin tsaruwar da wajan yayi shine yasakata tsallen dadi lallai zasu wataya cikin gidannan,Wani Dan madaidaicin falone Wanda aka shiryashi da wasu musulman kujeru masu numfashi sai kayan kallo da frij agefe Sam babu komatsai balle hayaniya cikin falon daga can gefene akai kofar kitchen dakuma wajan Dani daga gefe.

Kai komaifa yaji sai kofar bedroom guda biyu ko wanne anzubamishi kayan gado masu matukar kyau da daukar hankali gawani mayen k'amshi daya kewaye wajan gwanin dadi,Wani irin numfashi taja tare da fesarwa Kamin tace kai gaskiya nima auran zanyi,Saurin waigawa tayi taga babu kowa sannan ta rufe bakinta tana dariya.

Fitowa tayi tare da jawo kofar hasaso soyayyar Jidda da dadyn kawai take tana dariya wai gwarama kenan,ammadai batajin dadyn dantasan 'Dan soyayyane shi.

Da misalin k'arfe uku saura aka daura aurena da Dr.habeeb yanda wasu suka sanshi kokuma alhaji habibu duk sunanshine domin babban likitane saidai tuni kasuwanci ya danne likitancin Dan inba yaga buk'atarshi takai dinba Sam ko asbt be yadda ya lek'a.

Tunda ya usi yashigo yana shaidama mutanen gidan an d'aura sai kawai naji hankalina yai wani irin muguntashi musamman danaga kowa yasha manyan kaya anata washe baki.

Kuka nasaka tare da k'amkame hajiya Ina nanata banso ni bansan auran.

Itama kukan tasaka tanafadin"Wannan yaro baka kyautaminba da zaka rabanida takwara lokacinda banyi zatoba Dan Allah Ku kirashi ya janye aurannan harta k'ara wayau.

Nanfa hankula ya tashi ganin hajiya na kuka ga gida cike da surukai da jikoki ga 'ya'ya.

Dole aka Kira yaranta maza manya sukazo sukaita aikin lallashi amma da ta tubure saidai akirashi yazo ya keni ita tafasa bashi auran.

Bayan sallar i'sha,I zuwa lokacin harna Fara fita hayyacina sabida tsabar kuka,Haka aka shiryani Dan tuni motocin daukar amarya sun hallara abun mamaki waini Jidda akaima aure!!!Abune na mamaki ai,Saidai komai rubutaccene sannan kowane bawa be isa ya gujewa k'addarar da take akanshiba.

****""""""****

Banwani jima da kwanciyaba,Saigashi ya shigo,Hade girar sama data k'asa nayi dan karma yaga fuska.

Kallo daya yaimin ya Saki dariya me sauti dan har Mimi saida ta motsa.

Harararshi nayi tare da juyamishi baya"Yi hakuri matar zokiji bake nakema dariyaba kawaidai inayine sabida tsaro kiyi kiyi hakuri taso muje yau babu abinda zanyi miki insha Allah iyakata rungumarki ainima inada imani Jidda ,Nai miki wannan aikin jiya mezaisani damunki yau? Zomuje mu kwanta Allah bazanyimiki komaiba.

Murmushin dake kan fuskarshi yasani kasa gasgatashi danhaka marairaicewa nayi,Dady kace wallahi!!!

Wani murmushin ya Saki lallai yau gashi matarshi nasashi rantsuwa,Cike da nishadi ya furta"Ammadai ko wa innan tagwayen abari intaba ko?

Bakina na turo gaba,To Allah banzuwa ni nan zankwana.

"To naji har nan dinma nafasa tabawa tashi muje.

Duk da haka bakina adane nabishi shiko sai sakin mirmushi yakeyi.

Dan girman Allah dady karkamin komai wlh nagaji har yanzu jikina bedaina ciwoba kaji?

"Karki damu Jidda babu abinda zanyimiki kinji? Yi kwanciyarki.

Sauke ajiyar Zuciya nayi na gyara kwanciyata cikin jikinshi ina shak'ar kamshin da yakeyi.

Shima inajin yanda yakekuma shigewa jikina.

****

"Haulat inbaki shawara zakiji?

Saida taiwani das das da cingam din dake bakinta kamin tace inajinki.

"Kinga dai tun farko dama Dr. Habib betaba cewa yana sonkiba balle kince yanzu dayai aure ya yaudareki,Hasalima saidaga bayannan sannan yasan kina sonshi,Kuma tunda kika gayamishi yabaki hakuri harma da shawarar kisami miji daga masu nemanki kingadai ai be cucekiba,Amma yanzu idanunki sun rufe kina Neman cutar da yarinyar dabatajiba bataganiba,To inbaki saniba ki sani matar da ya aura marainiyace gaba da baya danbata da uwa balle uku,Wallahi kika tabata Allah bazai barkiba,Sannan nasan koda aikin da zai aureki akayimiki zai aurekin Amma wallahi bazaki taba samun kwanciyar hankaliba dan ba sonki yakeba,Danhaka dan Allah ki hakura tun kamin lokaci ya kure miki,Nikinga tafiyata.

Dawani kallon banza tabita bayan barinta dakin,Amma Sam maganganunta ko daya babu Wanda yai tasiri akanta.

50.

Cikin rashin kuzari ta tura kofar tashiga ranta amatukar bace domin duk abinda suka tattauna kusan akunnenta akayishi bata taba tunanin rashin hankalin diyar tata yakai hakaba.

Kallo daya haulat din taimamahaifiyarta taji hankalinta ya tashi domin mace ce Wadda Allah yayota tsayayya musamman akan yaranta.

"Tashi zaune dan ubanki kimin bayani dalla-dalla yanda Zan gane kamin in miki shegen bugu yanzu kamin wani cikin yayunki ya shigo insa ya karairayaminke wallahi ,Gara inyi jinyarki da masifar da kike Neman jamana gayamin waye Habib?

Tuni tafara hawaye yayinda cikin zuciyarta taketa tsinema aminiyar tata dan itace tajamata komai.

"Umma dan girman Allahkiyi hakuri wallahi na daina.

"Abunda na tambayeki kenan dama?

"A a  Umma shine wannan likitan da muke aiki k'arkashinshi wanda yataba duba hajiyar Abba lokacinda tai ciwo,Wallahi babu komai tsakaninmu.

"Dama ainasan babu komai tsakaninku domin mutun me hankali kamarshi bazai tsaya sauraran mahaukaciya Mara nutsuwa kamar kiba,Ke inbanda hauka wani shege yacemiki Awannan zamanin mace na cewa tanason namiji? Kila kallo namiji ma kezuwa yace yana sonki amma idan anyi auren ya ake k'arkewa balle kinkai kanki gareshi,Wai meyasa baki da nutsuwa ne haulatu?

To wallahi dagayau zuwa Rana itayau ki fidda mutun daya cikin masu nacin nemanki,Inba hakaba wallahi wallahi haulatu ina tausayamiki dan tabbas zanyima mahaifinki bayanin komai yabaki duk wanda yaga dama nagayamiki sati daya tal nabaki,Yo banda sakarci irin naki ga masu sonki wa inda basu damu da wulakancin da kikemusuba sudai fatansu kawai ki amince amma sai Wanda bemasan kinayiba,Kuma kinsami k'awa ta arziki tana gayamiki gaskiya amma kekina ganin bataimiki daidaiba!!! Yanzu Ke Saiki iya zuwa wajan wani katon banza yai miki asirin da zaki auri wani?Angyamiki so haukene?

To kiyi gaggawar fidda miji tunkamin incanza shawara ma wlh.

""""""

"Jidda Tashi ga ruwan zafi can nafara doramiki wanda zakiyi amfani dashi wajan girki kinji! Ko jikinne?

Manyan idanuna da sukadanyi surkin ja Sabida barcin da be isheniba na zube Saman fuskarshi dan har wani baya yaja sabida yanda kallon ya bigeshi.

Cikin shagwaba na kalleshi,Wallahi dady ko ina ciwo yakemin kumafa lafiyata lau amma jikina kamar ba nawaba.

Hannuwanshi ya daga sama"Sannu Ammadai ai ni babu ruwana ko? Tunda jiya barci kawai mukayi banyimiki komaiba ko?

Wani kallo na sakarmishi kamin ince Ai tunna shekaranjiyane ko.

Dariya ya Saki kamin yace"Amaryar dady sarkin rikici to kiyi hakuri zo inrakaki ki wanke baki saimuje inkamamiki girkin kinga yau juma'a nima zanshiga wajan aiki yau.

Hatta ruwan da Zan wanke bakin da kanshi ya zubamin shi,Duk motsina akan idanunshi,Yayinda yaketa furta sannu Allah yaimiki albarka jidda,Allah ya jikan su mama.

Nikuma wannan adduar ke kuma farantamin rai wlh.

Lallai ko yanzu naga ribar auren babban mutun kuma me shekaru,Dan duk tsiya sai ansami banbancin hankali da tunani tsakaninsu.

Bina yake kamar jela har saida na kammala komai naima Mimi wanka shikuma yaimata shafa ya shiryata, Ah dady baka shiryaba Kai?

Langabar da kanshi gefe yayi"Ai kenake jira jidda bazan iya shiryawaba.

Hijab kawai nasaka akan tawul din dake jikina na fice zuwa d'akinshi,Yayinda shikuma ya tura Mimi falo ya biyo bayana.

Numfashinya kawai naji saman fuskata,Har mamakin daddy nake wallahi.
Hijab din jikina ya zare yana kallon cikin idanuna niko bansan na lumshe idanunba sabida yanda gabadaya ya kashemin jiki.
Manyan idanuna na fiddo waje lokacinda naga yana cire kayanshi,Nan da nan naji hankalina yana nema yatashi,Amma saina daure ban nunaba,Humm wanka ko wasa,Haka yagama jagulani sannan muka fito ko idanuna kasa budewa nayi sabida kunya shiko ko ajikinshi,Saima mirmushi da yake saki duk lokacinda ya kalleni.

Ko wajan cin abinci kusan siriki haka ya zamemin dan wata irin masifafar kunyarshice ta addabeni bantaba ganin babban mutun babu kaya jikinshi ba sai yau.

""""

Bayan wata daya, Kwance nake saman doguwar kujera idanuna arufe barci nakeyi amma irin barcinnan Mara dadi.

Sadiq ne wajan kafafuna yanata matsaminsu,Sunyi dako dako dasu domin da zazzabi nakwana bawani barcin kirki nayiba ga dadyn benan yai tafiya akan kasuwancinshi.

Wayata daketa ring Sadiq ya dauka tare da gaida mahaifinshi dan dama shine yaketa Kira akai akai.

"Sadiq yaya jikin auntyn naku da sauki ko? Zahra din tazo kuwa?

Eh tazo daddy gatacan tana girki amma auntyn bata daina zazzabinba yaushe zaka dawo ne?

Jiyai hankalinshi yakuma tashi fiye da farko"Kaga Sadiq bani ita muyi magana tukunna kaji!!!!

"Daddy ai barci takeyi.

Kanshi ya dafe yana kallon Kamal dake gefenshi.

"Ka kwantar da hankalinka dan Allah baga hajiya can ka turaba insha Allah zata warware damma Allah yasa cikin hutu suke,Gobe idan Allah ya kaimu saika wuce,Nikuma idan ankuma kwana biyu na kammala ayyukan nan saina biyoka,Amma Anya ba cikine da itaba Dr.?

Wani zazzafan huci ya fitar kamin yace ina tunanin shine kamal ni wallahi tsoron fadan hajiya nakema kasan tace duk dibarar da zanyi inyi kadda inyima yarinyar mutane tun yanzu aita fama gara zuwa gaba,Nikuma inason haihuwa da ita bama hakaba wani lokacin sai Inga kamar zata iya barina Amma kaga idanmuka Tara zuri'ah da ita,Rabuwarmu zata iyayin wahala.

"Eh hakane kam,Ai kawai share maganar hajiya zakayi tunda da lafiyarka itama da lafiyarta arasa samun cikine Habib ai kawai fuska zakayi,Allah dai yasa tasami laulayi me sauki.

"To amin ya Allah danma yarinyar Nada kokari wallahi har mamakinta nakeyi wani lokacin.

"Eh haka naji nafeesa na fadi,Allah yakawo masu albarka dai.

**""""**

"Aunty dan Allah kitashi kiduba abinda nadafa ko zaki iyaci tunfa safe nazo gidannan amma har yanzu ko ruwa banga kinsama bakinkiba wannan yunwar mafa wani ciwonne,Cewar zahra.

Dakyar natashi zaune,Zazzabin ya sauka amma Sam banjin dadin jikina hasalima jinake kamar inta ihu konaji dadi,Zahra banjin dadi wallahi jikina kamar ba nawaba bakinama daci yakeyi.

Cikin tashin hankali ta koma gefe tare da dannama dadyn kira, Dama har lokacin zaune kawai yake danhaka da sauri ya yanke kiran ya kirata.
"Zahra ya akai?

Daddy takicin komai wallahi kuma jikinta ko kwari babu,Dazu har kuka tayi.

Jin yanda muryar zahran ke rawa yasasu sakin murmushi dan yasan indai kukane to suduka sukayishi.
"Bata wayar Bari inyimata magana.

Duk da nayi kewarshi amma jinai kamar infasa wayar dannifa jinake komai babu dadi.

"Babyn habibu ya jikin naki?

Cikin sanyin murya nace da Sauki.

Zamanshi ya gyara kamin yace"Sannu Allah yabaki Lafiya gobe insha Allah zanzo sai indubaki ko muje asbt,Amma yanzu ki taimakamin kici wani Abu kinji? Inkuma akwai wani Abu da kike buk'ata nadaban gayamin sai insa akawomiki kinji ko!!!!

Yamutse fuskata nayi kamin ince to.

Saurin ajiye wayar nayima dan kadda yakuma yimin wata maganar daban.

Kallona na maida akan zahra da tayi wata kalar tausayi da ita,Abincin ta kawomin shinkafa da miya wadda ta wadatu da nama saidai kallo daya naima abincin naji kyamarshi ta kamani,Danhaka da sauri na dauke kaina,Dan Allah zahra fitar da abincin nan wallahi ko ganinshi bansan yi.

Da sauri ta mike hartana kokarin faduwa"nashiga ukuna ni fatima zahra wai meke damunki dan Allah me kk so yanzu?

"Banidai lemo insha  kawai idan bakina ya warware naci abincin amma banjin dadin bakina Sam wlh,Inaga zazzabin da nayine kawai.

Muna cikin wannan artabun da zahra saiga sallamar hajiya kaka da kuma hajiyata da alama dayane ya biyama daya.



Dukansu da alamar damuwa suka k'araso ko wacce namin Sannu niko gwana saiwani bata fuska nakeyi,Dama yaya lafiyar kura.

"To ke takwara haka ake rayuwar duniya sabida Allah Dan naga da Alama kwanan nan zaki zama mama"

"Kai hajiya kibarmin diya ta wala gaskiya,Ai duk laifin na wannan shakiyyinne,Tunda har fada naimishi akan lallai yayi 'yan hikimominsu na likitoci kadda yai gaggawar yimata abunnan amma yai biris gashinan tun ba aje ko inaba za afara zarya asbt.

Kinjiki dawata magana komai ai na  Allah ne ke zahra kiramin usmanu yazo ya mik'amu asbt aduba kamin megidan ya dawo.

Bakina na turo gaba daya ,Allah banzuwa ni babu inda zanje bama wani wuri kemin ciwoba yunwa kawai nakeji.

"Humm aifa abin nema yasamu ke zahra samo Mata wani Abu taci,Cewar hajiyata.

Nidai lemo kawai nasha nasamu na kwanta yayinda suka dasa hirarsu saikace ba Mara Lafiya sukazo ganiba.

Sai yamma liss nasami sukunin farkawa,su hajiya kaka nanan har lokacin gabadaya sunhana gidan sakat DA hirarsu.

Wanka nayi tare dayin Sallah sannan zahra ta kawomin dambu Wanda hajiya kaka tasa ayomata.

Nadanci amma bada yawaba Dan har lokacin banjin dadin bakina.

Bayan sallar magriba ya usi yazo ya kwashesu gaba daya zasu biya su ajiye hajiya kaka saiyakai hajiya gida Sannan su wuce bayan yaimin alkawarin gobema zai kawo zahra din ta yini.

Adaddafe nai sallar isha'i Mimi na gefena gabadaya yaran basu DA walwala sabida ganina kwance DA sukayi.

Faruk ne ya mikomin wayata, DA kyar na amsa idanuna alumshe nasan dai bazai wuce daddy ba tunda dama kullun saimunyi waya kamin mu kwanta.

"Autar mata ya kike ya jikin naki?

Alhamdulillah naji sauki sosai ya aikin?

"Komai qalau baby gobe da wuri zan shigo insha Allah saimuga yanayin jikin,Ammadai kinci wani abun yanzu ko?

"Daddy banjin yunwa bakina babu dadi ni wallahi komai ya canzamin daddy.

"Ayya!! Yi hakuri zakiji sauki insha Allah bari harna dawo yanzu kisa Sadiq ya rufo kofar falon saiku kwanta kinji ko?

""""***"""""

Da wani irin kasala DA nauyin jiki natashi wanda yafi na jiyama,Abinda yai matukar tsoratani,Sadiq ya hadamana tea tsurarshi mukasha danshi ko kwai be iya soyawaba tea dinma ni na dinga gayamishi yanda zaiyi.
Gyaran gida da d'aki kuwa basu da matsala dan ina kwancennan sukai komai.

Bankumabi takan daddy ba duk da Inajin yanda wayata keta ring,Kuma nasan kila shine ko su hajiya.

***

Tunda nai sallar asuba na lallaba na kwanta kan abin Sallar wani irin tashin zuciya nakeji kamar zanyi amai amma Sam nakasayi har saida na gwammace inyi Kawai kona huta.

Zaune yake yayinda Mimi ta makalemishi har lokacin kallona yakeyi ganin yanda gabadaya na canza ko ina ya ciko naiwani jajir dani sai fuskatane datadan fada sabida zazzabin da nakeyi,Dalilin dayasa fuskata takuma yin wani haske ga karanhancina yafito sosai,So yake yai kissing din libs dina Amma Mimi takasa ta tsare tanata bashi labarin aunty babu Lafiya.

Jin maganarta saman kaina yasani bude idanuna,Aiko bansan na tashi zauneba,Shigewa nayi na wanko bakina,Sannan nafito naimishi Sannu DA zuwa,Rungumeni yayi ajikinshi ya na Sauke numfashi Dan sosai yakejin yai wata irin kewata balle yanda yaga jikina ya ga ma canzawa dinnan.

"Idanunshi kamar zasu fado haka yake kallona,Nikuma saima nadingajin kunyarshi musamman dana tuno tsadaddun kalamanshi gareni,Lokacin wannan tafiyar.

"Mimi jeki wajan yaya faruk bari inje inyima aunty allura ko? Ko kinaso inyi miki?

DA gudu tafice daga d'akin Dan atason allura ko kadan.
Ni kaina hankalina yatashi jin yai maganar allura.

Hannuna ya Rik'a muka nufi d"akinshi,Dan yafi tsaro acewarshi.

Marairaicewa nayi,Ganin yana tube kayanshi,Daddy Dan Allah kai hakuri bani da lafiya fa!!!

"Nasani Jidda na Amma nima yakamata ki tausayamin kinji nasha wahala

[5/9, 9:06 PM] Maman Dije: 52

Bansan lokacinda nafara sakarmishi hararaba lokacinda na tabbatar da abinda yake nufi,Kai lallai daddy ya iya naci da kunata Saikace tsohon maye.

Murmushi yayi tare da rikoni jikinshi yana sunsunar wuyana"Akwai zafi har yanzu jikinki kiyi hakuri inbawa shukata taki tukunna,Sannan inga kalar matakin DA zan dauka.

Turo bakina gaba nai ina harararshi,Nidai wallahi A a Dan Allah kadda kayi komai.

Ina kan cinyarshi yayinda yaketa shafar bayana idanunshi arufe,Niko tuni na lafe jikinshi ina sakin numfashi.

Saida ya tabbata ya kaini inda yakeson Sannan yasami nutsuwa nikam hadda kukan shagwaba na.

Matseni yai cikin jikinshi yana saukar da numfashi tare da shafar bayana,magana yakeso yayi Amma yakasa sabida wani irin mugun shauki dake dawainiya dashi,Jiyai yau komai zam har saida yasaki layi.

Da kanshi yaimin wanka, Niko saikuma lankwashewa nakeyi musamman danaji jikina yakuma saki fiye da farkon.

Ina kwance lamo zuciyata sai hautsinawa takeyi wani irin amai nakeji Amma Sam yaki zuwa,Shikuma yana tsaye  gaban madubi yana gyara fuskarshi.
Kallo daya yaimin ya fahimci abinda ke damuna danhaka da sauri ya k'araso wajena ya tadoni zaune"Amai kikeji ko?
Kaina na dagamishi lokacin har idanuna sunciko DA hawaye.

Dagani yai gabadaya ya jijjiga kamin wani lokaci aman yafito aiko dan ruwan lemon danasha saida nai amanshi sannan ya watsomin ruwa ya maidani ya kwantar nidai nishi kawai nake Saki Dan amai beda dadi.
DA kanshi ya gyarawajan lokacin har anfara kiran Sallar LA'asar,Agurguje yafice danya sami jam'I nikuma nagyara kwanciyata.
Saidai kamin barcin yaigaba dani naji sallamar su hajiya hadda zahra kamar jiya.

Dole natashi nakoma falon lokacin nai zuru zuru dani saikace wadda ta shekara tana jinya.

Duk sannu sukaimin bayan mungaisa.

Wata irin mummunar faduwar  ta sameshi lokacinda yaga direban gidansu,Ya tabbata hajiyarshice gidan,Fadanta ya tuna DA kashedi akan karyaima jiddan ciki da wuri,Wani miyau ya hadiye jiyake kamar kadda ya k'arasa falon Saidai Ina yasan hakan bawai me yiyuwabane.

Jiki asanyaye yai Sallama falon,Jiyai kamar yai kwana lokacinda yaga hadda hajiyata Sam beyi tunanin hakanba gakuma zahra DA wuri yafara Adduar Allah yasa kadda hajiyarshi ta tsinkashi gaban yarannan.

Saidai kamin yakai idashen tunanin yaji tanafadin"Sannu habibu kajiko sannu nace maka"

Zama yai k'asa tare DA gaidasu,Nikuma lokacin jinai maganganun da sukeyi sun isheni shiyasa saina lallaba na shige daki zahra ta biyoni.

"Sannu habibu Sannunka kaji!! Kai yanzu sabida Allah menagayamaka game da yarinyar nan duka nawa take dazata fara fama da wannan lalurar koba  cikine da itaba? Cewar hajiya kaka.

Kuma marairaicewa yayi hankalinshi nakuma tashi da fadan hajiyar dan Akwaita da Sababi idan taso.

"Hajiya har yanzu ban tabbatar ba Amma zuwa da yamma sosai zanje da ita asbt,Sai aga mene.

Hannuwanta ta watsamishi alamar dak'uwa kamin tace,Kajiko gidanku nace maka, Dazakace wai baka tabbatarba anya habibu,To ai shikenan kaima kaji ajikinka ai.

Nan suka kacame hirarsu hidai yana gefe zaune Saidai hankalinshi nawajan d'akin dana shige,Tunanin yanda jikin nawa yake yanzu.

"Wai bebaki magani bane daya dawo? Naga kamar ma idanunki sunkuma zurmawa yau bakamar jiyaba!!!

Lumshe idanuna nayi ina tuno murzan da yaimin dazu Wanda har Saida naji tsigar jikina taiwani yarrr, Uhumm daddy akwai bakin wayon masifa.
Kallonta kawai nayi Amma bance komaiba Saima rufe idanuna danayi,Nifa jikinne nawa gabadaya yasaki banjin dadinshi.

Saida aka kira magriba Sannan suka wuce ko wanne da tsarabar da yaimin.

"Aunty  inkawo Miki lemon ne zaki k'ara?Cewar Sadiq.

Riko hannuwanshi nayi inajin kamar insami saukin wannan ciwon adalilin haka.

Zama yai gefena yai shiru wani irin tsoron mutuwa yakeji tunda suka rasa umminsu Sannan ga aunty dinsu itama yanzu kwance babu lafiya"Allah yasa ki kasance damu aunty.

Kallonshi nayi Sainaga hawaye kwance afuskarshi,Sainaji hankalina yatashi Allah yasani ina sonsu kamar yadda suma suke sona nasan kuma duk YARDA ce sila.

Kusan asakwane yashigo dakin Mimi da faruk na biye dashi ashewai Sadiq suketa nema basuganiba danshi beje sallar magriba dinba.

Cikin Sanyin jiki ya kalli Sadiq din kamin yace "Tashi kaje kai Salla munata nemanka Sadiq.

Shigar dani tayi cikin jikinshi bayan barin yaran dakin,Sannan yace tashi muje ki fitsari indan Sami kadan kinji ko!!!

Positive,Shine sakamakon awon da yaimin aiko nan da nan ya rude da murna DA farinciki duk da cewa eh damafa yai tunanin hakan.

Tun daren nan yaima yaran Albishir da samun k'ani ko k'anwa aiko saida yai danasanin fadin domin gabadaya suka hanashi sukuni kowanne yana fadin abunda yakeso ahaifa kai daga karshema duk wajena sukace zasu kwana.

''''''''''''

Za aimiki aiki wanda zaki shiga gidanshi kota wani haline Ammafa zuwa gaba akwai matsala idan kin amince da hakan ki zube abinda ke jakarki ayau za afara aiki zuwa juma'a ko asabar adaura aure.

Jin kanta take kamar wata sarauniya sabida yanda labarin yazo mata,Babu tunanin matsalar daya gayamata zata iya fuskanta kawai ta furta ta amince,Danhaka ta juye abinda ke Jakarta tare da jaddadamishi tana tafe jibi domin Amsar sakonta.
[5/9, 9:06 PM] Maman Dije: 53

Ni Sai inga kamar kinyi wauta khairat domin nifa nan bawani yarda da malamannan nakeyiba sabida koda kasami abinda kakeso zuwa gaba dole sai wata matsalar tataso danhaka ni ashawarata kawai kiyi hakuri tunda kinada masoyanki ko?

"Haba zee ya zaki dinga magana kamar bakisan wacece niba? Ke kintaba k'areba Dr.kallo kuwa kinga abinda nake hangowa?
Bama wannan ba ni danyacemin DA matsala wallahi babu ruwana kome zai faru ya faru indai nashiga gidan,Dan yarinyar ma waje zanyi da ita.

"Hummm ke matsalarki kenan khairat Sam bakison shawara amma yunzu sabida Allah harma yacemiki akwai matsala Amma KO ajikinki ko?

"Hummm kedai kawai ki saki jikinki asha shagali kilama babu wata matsala sharrine kawai irinnan malamannan.

""""

Amma Auta kana ganin babu matsala zaman jidda gidannan daga ita sai yara ga laulayi?

"Hajiya babu matsala insha Allah,Ai kinga bakoda yaushe ne bani gariba Sannan asbtn ma ba koda yaushe nake zuwaba Zan kula da ita insha Allah.

"To ai nidai ina gayamakane kadda kaje kai washagare DA yarinyar mutane azo nan gaba Ana kiran wallahi tallahi.

Babu komai insha Allah hajiya Ina sonta sosai Ina buk'atar abunda ke cikinta Zan kula DA ita.

Murmushi tasaki tana kallonshi,Musamman data tuna lokacinda yake ciccin magani magani akan auren"yo tundafa kasami kamar Jidda ai dole kasota habibu"

Akunyace ya dauki kular shashshakar dake gabanshi yabar gidan yana murmushi.

**""""**

"Babyna tashi ga abinda kikeso ansamo.

Yamutsa fuska nayi kamin intashi zaune,DA kanshi ya kaini na wanke baki Sannan nazo na zauna.
Kallon Sadiq nayi tare DA bashi umarnin dauko abincin mukoma falo domin cikin Dakin daddy muke.

Tare da yaran muka cinye wannan Abu tas yana zaune saman kujera yana kallonmu ya na matukar jin dadin ganin yanda gidannashi yake yanzu.

Dayake naci na koshi sainaji nadan sami nutsuwa,Dan dama hadda yunwa tunda bawani abincin kirki nakeciba.

Kamin wani lokaci kowanensu yafara bani labari musamman dasukaga har dariya inayi.

Kwance yake idanunshi arufe Amma yanajin dukkan abinda mukeyi yayinda zucuyarshi ta cika da farinciki fuskarshi ta yalwatu da murmushi.

"Faruk daukomin wayata gatacan Ana kira"

"Hello zahra"

"Na'am aunty ya  jikinki Ashe baby muka samu, Ta idasa maganar  muryarta cike da farinciki.

Kirjina yaiwata irin mummunar bugawa,Dan bansan natashi zauneba saidanaji muryar daddy na fadin Bi Sannu Jidda.

Hannuna nasa na dafe kirjina inajin wani irin zullumi dake baibaye zuciyata.
Sai lokacin na tunada ance alamun samun ciki shine daina al'Ada nikuma tun zuwana gidan daddy so daya kawai natabayi ni nama manta anawani yi.
[5/9, 9:06 PM] Maman Dije: 54

Wani irin miyau na hadiye kamin in ajiye wayar batare damungama magana da itaba.
Idanuna akanshi kallon da bantaba yimishi irinshiba sabida yanda hankalina ya daga gabadaya 'yar kunyar nan ma saina nemeta na rasa so nake kawai inji muryarshi ta na k'aryata maganar zahra din Saidai banga alamar hakaba Dan tuni shima hankalinshi yatashi dajin abinda zahra din tace domin yana kusa Dani sosai ta yanda zai iya jiyo me akecewa.

Tashinai tsam na wuce d'akina ina danne kukan dake tasomin dan sosai hankalina yatashi cikin k'ankanin lokaci.

Da saurinshi yabi bayana yanajin babu dadi cikin ranshi Sam beso nasan da cikin ba yanzu.

Hankalinshi yakuma tashi ganin yanda nake kuka ina birgima.
Rungumoni yayi jikinshi yana lallashi Amma Ina kukana kawai nakeyi.

"Jidda wai kukan me kikeyi hakane kinason kijama kanki wani ciwonne banda Wanda kikefama dashi?

Cikin kuka nace wallahi bansan ciki ya za ai ace ina k'arama dani haka Zan haihu ni Allah banso namafasa zama dakai gida zankoma.

Hannunshi yasa ya dafe kanshi kamin yafara magana ahankali"Kinga kwantar da hankalinki waye yace kinada ciki dagayin ciwo,Ni hauka nakeyi DA zanyimiki ciki tun yanzu? Ki kwantar DA hankalinki saikin gama makaranta zamuyi cikinmu kinji ko?

Tuni kukana ya d'auke,Daddy DA gaske?

"Eh mana ba yanzuba saimungama soyayyarmu jiddana.

Cikin shagwaba nace to daddy kacema zahra tadaimin irin wannan wasan wallahi harnaji tsoro.

Maidani cikin jikinshi yayi,Tare da saka hannunshi cikin rigata yana shafar lafaffiyar marata tuni ya lumshe idanunshi yanajin wani irin so DA kaunar abinda ke ciki,Lallai yafi kowa sa'a gashi Allah yabashi wani rabon lokacinda be zaci kuma samun waniba.

Lamo nayi jikinshi ina sauke numfashi musamman jin yanda yakemin wani waiwayi cikin cibiyata.

Jin tahowa yyasashi dagani daga jikinshi ya gyaramin zama tare da sharemin hawayena,Yana murmushi,Yayinda cikin zuciyarshi yake jinjina rikici kalar nawa,Musamman ranar da nasan akwai ciki jikina.

Shigowar Mimi yasani mikewa na wuce toilet jinake zuciyata na tashi Amma ba irin sosai dinnan ba.

Fita zaiyi amma saiya leko wajena,Yaganni tsugunne cikin bandakin.
"Subhanillahi Jidda mene haka kuma?

Daddy amaifa nakeji shine natsaya jira yafito.

"Sorry taso bazakiyiba ttashin zuciyarne kawai,Damme zaki zauna cikin bayi haka kawai taso muje ki kwanta Ki huta zakitashi da sauki kinji ko!!!

""""

Nidai bazance ga abinda yafaruba Amma zahra batakumamin maganar cikiba tsawon kwanaki biyu DA suka biyo baya danhakama sainai tunanin kila damadai tsokanace irintata.
Amma kullun tana kirana taimin yajiki,Hakama hajiyata da kuma hajiya kaka.

Shiko uban gayyar ai ko motsinayi saiya tambaya matukar ina gidan,Sannan har yanzu bekuma neman hakkinshiba musamman dayaga jikina yai laushi duk da cewa inasamin sauki sosai.

Saidai ina mamakin yanda jikina yake canzawa musamman kirjina dayake kuma cikowa,Amma sainai tunanin kodan daddy na musu shan anatsine uwar me karyane,Dan sosai beda sauki awannan bangaren.

***

Tunda nafito wanka idanunshi na kaina dama gidan babu kowa dagani saishi ,Yau sunyi gidan zahra.
Turo bakina gaba nayi ganin yanda yake kallona ko kiftawa besonyi gashi saiwani lasar libs dinshi yakeyi saikace meshan sweet.

Murmushi yasaki ganin abinda nakeyi, Jiyai ko ina na jikinshi ya motsa wata irin sha'awa tatasomishi,Dandama anjima Ba a haduba.

"Zokiji Jidda"

Harararshi nayi tare da mak'ale kafada dannasan sauran zancen,Musamman yandanaga yawani baje agadon.

Murmushi yasaki tare da tasowa zuwa gareni,Niko nafara kokarin rugawa waje.

Dariya yake sosai sabida ganin yanda narude"Lallai jidda dadyn akeyima wannan gudun saikace nazama dodo bama wannanba bafa cinyeki zanyiba kadan Zan dangwali arzikinki Autar

mata Amma kina niyyar guduwa.

Luf nayi cikin jikinshi ina zare idanuna dannasan shikenan kuma yanzu zai shammaceni ya lamusheni tas.

Dakyar na kwaci bakina nasami halin furta daddy Ahankali Dan Allah.

Murmushi yadan saki yana tunanin ranar DA zansaba da wannan abun.

Sosai yai k'okarin rike girmanshi danbina sannu,Amma hakan be hanani yimishi kukan tabaraba,Kukan dana lura yana matukar yin tasiri cikin zuciyarshi.

Lamo yayi yanasakin numfashi guda-guda dan sosai yasami nutsuwa,Dan ahakama jiyake kamar ya koma dandai tausayina dake lullube cikin zuciyarshi.

Lallai kowace mace da kalar baiwar da Allah yaimata,Duk da yakasance ba manemin mataba,Amma ya tabbata jiddanshi nacikin mata na musamman da Allah yaima baiwar ni'imar gamsar da namiji,Shikadai yasan halin da yake tsintar kanshi aduk lokacinda ya kebe da ita,Samun kanshi yayi da addu'ar Allah ya Kara tsaremishi gonarshi ta haramta ga kowa inbashiba.

Saukar halshenya cikin kunnena yasani sakin ajiyar zuciya tare da k'ankameshi,"Murmushi yasaki kamin yace"Allah yaimiki albarka jiddana Allah ya k'aramiki hakuri da juriyar kula dani,Ammadai yau babu zafi ko?

Boye fuskata cikin kirjinshi nayi tare da turo bakina gaba"Eh mana akwai zafi"

. "Kai jiddana Ammadai ba sosaiba ko? Kadan nayifa ko isatama beyiba naji tausayinki na hakura shine zakice DA zafi kodai Ind'an k'arane?

Kukan shagwaba nasakarmishi ina Mirza kafafuna dake harde cikin cinyoyinshi.

Wata dariyar nishadi yasaki kamin ya gyaramin kwanciyata"To shikenan yi hakuri nafasa kinji ko? Laifinkine Jidda har yanzu kinkasa sakin jikinki dani munfa riga munzama daya babu komai tsakaninmu yanzu sai YARDA da Aminci bazan cutar dakeba zanyi iyabakin kokarina wajan farantamiki insha Allah danhaka ki saki jikinki dani kinji? Ko wannan zafi-zafin da kikeji nasan tsoron da kikasama kankine Amma inda zakidaina jin tsorona tabbas zakidaina jin zafi saidai dadi ai kinaso ko?

Boye fuskata nai cikin jikinshi ina dariya,Kai daddy ko!!!

Da kanshi yaimin wanka kuma ya shiryani bunu-bunu yaimin sannu saikace wadda tasha aiki.

"Yanzu ki saka wannan doguwar rigar saimufita ko zakiga abinda kikeso ko?

Da murna na mike dan sosai naji dadin jin cewar zamufita.

Muna tsakiyar falo hannuna cikin nashi mukaji kwankwasa kofar falo.
Sakin hannunayayi tare da cewa jirani nan inzo.

Kallo daya yaimata yaji wani irin mummunar faduwar gaba ta sameshi.
[5/9, 9:07 PM] Maman Dije: 55

Wani irin masifaffen dadi taji musamman data lura da yanda yasha jinin jikinshi.
Hannunta ta mikamishi tare da furta khairat Usman by name"

Dakyar yasamu ya daure be bata hannunba dan wani irin kwarjini yaga taimishi,Murmushi ya sakarmata,Batare da yayi maganaba.

Ganin bazai bata hanya ta wucebane yasata furta"Dama inason yin magana dakaine idan babu damuwa"

Samun kanshi yayi dabinta kamar yadda ta buk'ata bayan yajawo kofar falon.

""""

"Nasan zuwa yanzu ka manta dani,To kamar yadda nagayamaka sunana khairat Usman muntaba yin aiki dakai shekaru biyu DA rabi dasuka wuce cikin asbtnku,So tun lokacin nakamu da kaunarka kuma nai kokarin nunamaka awancan lokacin saidai Sam baka aminceba,To gani nazo akaro na biyu inafatan zaka amince min awannan lokacin?

Wani irin miyau ya hadiye Wanda besan kona meneba Amma saiya nuna babu komai azahiri,Domin wani murmushi yasakima,Tare da furta" Karki wani damu insha Allah babu matsala,Saidai inada iyalifa ba kamar Sanin da Kikaimin bayaba.

"Babu komai karkawani damu ai nasan komai akanka dan Wannan matar takaba ai bata wuce rainoba itaba Dan haka zanhada nakula dasu duka kamin tazama mace.

Murmushi yasaki,To shikenan nagode muje in ajeki sai inga gida kilama zuwa dare ki ganni inafatan babu matsala ko?

"Laaa babu komai wallahi muje,Nida nakeson hakan!!

****

Gajiya da tsayuwar jiranshi nayi nakoma na zauna tunanin inda yashige nakeyi daga Bari inzo.

Wani takaici ya danne zuciyata ganin har anyi magriba gida nikadai saikace mayya.
Sai kusan sallar isha'i Saiga ya usi ya maidosu su Sadiq,Sannan nadan sami sukuni Amma duk DA haka hankalina bekwantaba dan tunanin inda daddy yashige yananan like cikin raina.

Tun Muna hira har Mimi tafara tambayar Ina daddy,Sannan suma sauran,Daurewa kawai nayi na furta yaje yadawo.

Bashine yashigo gidanba saiwajan Tara dawani Abu nadare.

Duk yanda naso muhada ido dashi Sam kiyai dan sosai ta bangarenshi yakejin Sam babu dadi Sannan kamar be kyautaba abundayayi.

Koda yashiga yin wanka be fitoba saidai yai zamanshi,Shiyasama yau hirar batai armashiba tuni yaran sukai min sallama sukai kwanciyarsu,Nima ganin zaman ba alheribane gareni yasani wucewa dakina nai kwanciyata Dan tuni zuciyata tagama hasala da abinda dadyn yayi yau.

Bak'aramin tsoro da mamaki nayiba lokacinda asuba tayi na tabbatar cikin dakina nakwana domin nasan duk wuya bekwana shikadai yanzu KO nayi barci saiya daukeni ya maidani d'akinshi Amma yau  jiya beyi hakanba Anya lafiya kuwa?

****

Bayan sati daya;.Abu kamar wasa saigashi yazama gaske,Cikin kwanakinnan munshiga tashin hankali musamman nida Sadiq domin shine babba kuma me wayau shine yasan meyake faruwa cikin gidan yanzu.Sam daddy beda ookacinmu yanzu besan zama gida idanma munsamu ya zauna to yana cikin d'akin shi yana waya abinda yaimatukar tasarmin DA hankali lokacinda na fahimci eh dafa mace yake waya, ko makwanci yanzu mundaina hadawa,Sabida be nemeniba nikuma banje gareshiba.
Tuni nafara figewa ga wani shegen zazzabin dare dayatasoni ga damuwa gashi yau Saura

kwana hudu mukoma makaranta,Tunanina anan wazan gayamawa wannan damuwar?

"Aunty wai kinaganin haka zamu zubama daddy ido?

"Uhumm To Sadiq ya zamuyi mishi tunda ba yarobane balle muce zamununamishi hanyar data dace nikam gaskiya abunnashi yafara bani tsoro kana kallo yanzu ko gidannan beshigowa saimunyi barci to yazamuyi mishi?

"To aunty ki kira yaya zahra saiki gayamata sannan agayama hajiya kaka kinga baki da lafiya,Wallahi bakiga yanda kika komaba kumafa shekaranjiya da aka aiko kiranshi wallahi ina lekawa wata mace nagani yanafita sukashige mota.

Shawarar Sadiq nabi nakira zahra saikuma akai sa'a tace taje wankin kai Amma gatanan zuwa.
Shiru nida Sadiq kowa da tunanin dayakeyi,Yayinda faruk DA Mimi keta wasansu cikin falon.

""**""

Innalillahi munbani aunty yaushe daddy yakoma haka? Wane irin abun kunya yakenema yajamana yanzu kuma?

Tsaki yasaki kamin yace kemadai kinfadi wallahi Saima kinga shegiyar matar dake zuwa wajanshi haushi zai kasheki,Ga aunty bata da lafiya Amma babu ruwanshi,Cewar Sadiq yana huci.

Matsowa tayi kusa dani,Dan girman Allah aunty kiyi hakuri nasan duk nice najamiki wannan damuwar Amma inshaAllah komai zai wuce bantaba tunanin daddy zaiyi hakaba kai anyama kanshi daya kuwa?Bama wannan mezaijamishi kula wata mace yanzu alhalin yana zaune dake? Dan Allah kiyi hakuri kutashi muje gidan hajiya kaka Dan gaskiya abun yayi yawa,Kai Sadiq jekacema isiya ya fiddo mota zamu fita.

***

Subhanillahi kai kutsaya bansan shirme duk yaushe hakan tafaru baku gayaminba?

"Hajiya kaka nimafa yau naji labarinnan wallahi.

"Tab to wallahi bazata sabuba ni kaina naga sauyi akan habibu Amma dana tambayeshi saiyacemin ai sabida yanayin aikine To Amma akwai matsala dan wallahi ni binta ban haifarma wata diya mace Dan dazata juyaba Allah kagani banshiga tsakanin surukata DA dantaba sannan bantaba sama matan yarana idoba, To aikuwa babu tsinanniyar da zata juyamin kan yaro.

Duk idanu muka zubamata musamman damukaga harwani huci takeyi kamin wani lokaci tatashi hankalin yaranta da waya akan azo atahomata da habibu duk inda yake.

"Kiyi hakuri jidda kuma ki kwantar da hankalinki mijinki ya hadu da Shu'umar mace Amma ki kwantar da hankalinki komai zai warware da iznin Allah,Kuma irin wannan ma Jidda ai da wuri ake fadin irin wannan matsalar Dan Allah kadda kikumayin Shiru kalli yanda kikarame kik karefa?

56

Nidai tunda hajiya kaka tagama sababinta saina wuce dakinta na haye gadonta danfa sosai nakejin jikina ya canzamin gakuma cinkushewar zuciya data addabeni da zafi itama.

Wasu hawaye masu dumi naji sun sakkomin tunanin irin halin danashiga Ashe dama haka mutun yake fuskantar qalubale kala kala Idan yai aure? Dama wannan dalilin kesawa duk wanda zaimaka fada saidai yace kai hakuri,Kai hakuri,Kowadai kai hakuri?
Tunanin ya usi ya fadomin danhaka da sauri na lalubi wayata na dannamishi kira.

Bawan Allah kamar dama jiran kiran yakeyi Dan da sauri naji ya d'auki wayar"K'anwata kin yini Lafiya ko?

Kuka nasakamishi hadda sheshsheka.

Innalillahi,Meyafaru menene na kuka kuma jikinne ya dameki?

"Yayana kazo ka d'aukeni ka maidani gida bansan daddy yanzu bazan iya zama dashiba kaji?

Tashi zaune yayi daga kwanciyar da yake tuni hankalinshi yakuma tashi,Dama babu dadewa ya kira wayar zahra yaji muryarta da alamun tasha kuka"Kinga Saurara muyi magana Jidda kina gidanwa yanzu?

"Ina gidan hajiya kaka nidasu zahra.

"Ok to jirani inzo yanzu Amma kidaina wannan kukan kinga baki da lafiya kadda damuwa taimiki illa yanzu zanzo saiki gayamin komai kinji ko?

Banwani jimaba saiga wayarshi,Wai yana harabar gidan hajiyar.

Hijab dina nasagala na fice duk da su hajiyar na falo Dan haryanzu bata daina fadaba tahana kanta sakat.

Tuni zuciyata takuma karyewa musamman danaga yayannawa cikin damuwa,Dannikaina shaidace akan irin son da yakemin be hada soyayyata data kowaba.

Shigewa nayi jikinshi inawani kukame matukar ban tausayi.

Rungumeni yayi jikinshi yanajin wani irin danasanin auran da akaimin tun yanzu,Dan yasandai matsalar bazata wuce akan auranba.

Saida ya lallasheni Sannan nagayamishi dukkan abinda ke faruwa,Hankalinshi yatashi amma tunani nafarko dayazomishi shine anya dadyn qalau yake kuwa?

"Jidda kodai kinyimishi wani babban laifine yake hukuntaki ta hakan?

Ya usi banyimishi komaiba har yaran yanzu babu ruwanshi dasu,Wannan macen ce kebiyoshi har gida ta janyeshi.

Munanan zaune ya usi nakuma lallashina saiga yayan daddy dakuma shi kanshi daddy din da alama tasoshi yayi.

Wani irin mummunan tashin hankali yaji lokacinda ya hangeni jikin wani rungume,Tsabar kishi,Saida yamatso sannan yagane ya Usman ne Amma duk da haka zuciyarshi bata sassautamishiba musamman dayaga yandanakekuma likewa jikinshi.

Ya Usman na kokarin gaidashi,Shikuma ya na kokarin rikoni,Aiko na makemishi hannu tare da harararshi danwani irin mugun haushinya nakeji.

Janyeshi Alhajin yayi suka wuce yanamai fadan"Damme zakace zaka janyeta ita da yayanta,Tunda kai kasata bakinciki aidole shi dan uwanta yasata farinciki kuma ya lallasheta tunda yanasonta.

Bakinshi ya tsuke kamin yace"Kuma kawai danyana yayanta saiyakamata ya wani kwakube,Kuma ainima iinason abata ko!!

"Kinga wuce gida nasan hajiya kaka zata dauki mataki akanshi kome akeciki saiki gayamin Amma kidaina kuka,Zandawo anjima daukar zahra saimuyi magana kinji ko?

Kaina nadagamishi tare da barin jikinshi na nufi falon hajiyar.

***

Mugun kallon data wurgamishi yasa yaji har hanjinshi saida suka motsa,Danhaka da sauri ya sadda kanshi k'asa yana zullumin abinda ka biyo baya.

Saida tagama karemishi kallo kamin tace" Ah lallai jin dadin duniya wato kai habibu wulakantani kakeso kayi a idon duniya ko?
To wallahi bakaji da kyauba danninan DA kakeji da gani nafi karfin wannan,Kai bama wannanba wace shegiyace kake bibiya yanzu  dahar tasa kake wulakanta iyalinka iyi?

Kanshi akasa yake tauna maganar da zaifadi danyasan bawai jin dadibane zai biyo baya ba tsakaninshi da hajiyar," Uhum hajiya dama watace nake nema kuma auranta zanyi!!!!

Wani irin jirine naji yana neman kayar dani dan sosai maganar tai matukar bugarmin zuciya.

Baki bude hajiyar da Alhajin ke kallonshi jin yanda maganar tazomusu amatukar bazata.

Kamar kazar da kwai ya fashemawa aciki haka na idasa shiga falon harwani ganin biyu biyu nakeyi bantaba tunanin haka nakeson daddyba sai yau.

Duk maido hankalinsu kaina sukayi amma bankalli kowaba cikinsu na wuce, Dan sonake in

dauko wayata da jakata inwuce gidanmu nagama zama da daddy koda sonshi zai kasheni kuwa.

Kayana ahannu nafito saiwani ganin uku hudu nakeyi,Kallo daya sukaimin duk suka mike tsaye sauri nakesonyi dan infice batare dawani yaimin maganaba,Saidai kashh wani jirine ya watsar dani batare danayi tunanin hakanba.

[5/9, 10:12 PM] Maman Dije: 57

Wani irin tsalle yayi saigashi gabana,Saidai hakan besa yasamu damar tabaniba kamar yadda yai niyya Dan tuni hajiyakaka taimishi wata ingiza saida ya hantsala Dan beyi zaton samun hakan daga garetaba.

Ruwa suka fara shafamin afuska saida nafara numfashi sannan takamani zuwa tsakiyar falon.

Kwanciya nayi tare da rufe idanuna Dan wani irin barci naji yana lullube idanuna.

Tsayuwar yagaji da ita Dan haka ya lallaba yakoma gefe ya Zauna Amma hankalinshi nakan kirjina yana kallon yanda numfashina ke hawa da sauka,Tausayina ya mamaye zuciyarshi musamman dayaga fuskata takuma komawa k'arama saidai akwai wani sihirtaccen kyau danakara ga cika da kirjina yayi,Yasan albarkacin tayin dake maratane.
Samun kanshi yayi dason jin dumina Amma yasan hakan bame yiwuwa bane,Sannan shi kanshi sai yanzu yakejin haushin kanshi da abinda ya aikata Sam zuciyarshi bata kyautamishiba.

"Wallahi habibu kafita cikin idanuna in rufe,Karka yadda musaka kafar wando daya dakai indai kanason zaman lafiya,Kodayake wannan ba abin damuwabane dannasan bawai cikin hayyacinka kakeba Amma duk da haka ubanwaye yaja?Gakuma kullun aikina kenan akan tunamuku riko da Addua musamman na tsarinjiki wa inda Annabinmu yabamu sabida irin wa innan masifun Amma bakuyi sabida kuga 'yan karshen zamani wai addua wannan tagagari bawa sabida Allah? Sai masifa ta afku aita tsalle-tsalle alhalin sakacin duk namune!!! Adduar fita gida ta gagari mutun? Inzaka kwanta shima ta gagara adduar maraice da safiya duk mutun yagaza yinsu Saiku dinga rayuwa haka kawai Kara zube,Ni shikenan bazakubar zuciyata ta hutaba habibu? Alhaji yatafi yabarni cikin duniyarnan me cike da rudani da tashin hakali.

Duk matsowa sukai gareta ganin tana kuka abinda basu saba ganiba,Sannan karshen musifa shine kasanya iyayenka zubarda hawaye matukar bana farinciki bane.

Hakuri sukaita bata har saida tafara sauke ajiyar zuciya Sannan Alhaji Yusuf din yace zaije yadawo.

Shima daddyn mikewa yayi da niyyar ficewa.
Saidai tuni ta katsamishi tsawa"Zonan zauna Dan ubanka gidan uwarwa zakaje kamike tsalau tsalau dakai kamar zakara yasha ruwa,Wallahi ka kiyayeni,Bama wannanba kaga habibu ina tausayamaka idan wani Abu yasami yarinyar mutane wallahi babu ruwana,Kuma ka zauna nan babu gidan ubanda zaka kuma zuwa sainagama daukar mataki daganan inga Mara kunyar da zatazo harnan tajaka, Kuma ka zauna karka dage da addua tunda kaima kazama talasuru.

Dolenshi yakoma ya zauna yana zare idanu,Dan hajiya kaka badai masifaba ga bakar mita saita yini maganar Abu misamman idan yabatamata rai.

***

"Kindaisan bancika son kukaba zahra so kikeyi kita tadamin hankaline da wanne kikeso inji? Jidda na cikin damuwa har yanzu zuciyata bata daina zafiba sabida yanda naganta kekuma yanzu kinzo kin tasani da kuka na tambayeki kinki magana kasheni zakuyi ne?

Kuma lafewa jikinshi tayi tana sauke ajiyar zuciya tunanin ta inda zatafaramishi bayani takeyi, Itadai daddy be kyauta mataba wallahi.

"Kayi hakuri daddyne duk ya jagula komai bansan zaiyima Jidda hakaba gashi bata DA lafiya Amma hajiya kaka zata dauki mataki.

"Karki damu kanki zahra,Tsakanin mata da miji sai Allah babu me iya shiga tsakaninsu kina nan kina kuka kilama sun daidaita kansu babu gidan auren da babu sabani cikinshi danhaka kima daina damuwa,Daddy nason Jidda haka itama tanasonshi kosun sami matsala zasu daidaita kansu tunda shidin ba yarobane balle ya biyemata,Damuwar da kika ganni cikima tunanin ramar danaga tayi nakeyi ga laulayi bazanso hajiya ta ganta ahakaba.

Kwanciya tayi jikinshi kawai ta gamsu da maganarshi Amma har lokacin tanajin zafin daddyn cikin zuciyarta.

""

Yauwa sannu Jidda tashi ki Salla saikici wani Abu kila kinji dama dama saikisha magani Allah yabaki Lafiya yarabaki da abinda ke damunki lafiya.

Tashi nai zaune Sai idanuna suka sauka akan daddy dake zaune akan sallaya da alama sallar ma batabari yafita yayitaba,Harara na wurgamishi hadda murguda baki, Saidai yai murmushi kawai yacigaba da tasbihin da yakeyi.
[5/9, 10:12 PM] Maman Dije: 58

Yauwa ga wannan kisamu kisama cikinci ko Allah yasa adace ya zauna Amma kidaina damuwa dan Allah, Cewar hajiya kaka wadda ke lallashina bayan nagama salla.

Juyawa tai ta wurgamishi harara ganin yanda yake kallonmu.

Yana cikin samuwa Amma hajiyar taki fahimtar hakan acewarshi,Balle dayaga yaran kamar ma gudunshi sukeyi wai hadda Mimi uwar 'yan kulafuci,Amma yanzu shareshi takeyi saima nanike jiddan da sukeyi, Gashi konan dacan hajiyar taki bashi damar zuwa.

****

Kai gaskiya bazata sabuba wallahi,Nawa nakashe akaimin wannan aikin Amma gashi komai na nema ya lalace tun kamin aje ko ina.,To aiko wallahi bazai sabuba.

Itakadai ke sababinta sabida tun safe take kiran wayar daddyn Amma har la'asar babu wani bayani daga karshema saitaga ashe kashe wayar yayima.

TO DAMA AI HAKA RAYUWAR TAKE MAGANAR BOKA KILA WA KALACE INKA YADDA KA BACE SANNAN BA LALLAI KASAMI ABUNDA KAKESO DAN SUMA MASU NEMANE.

Bayan Sallar magriba;
Ganin irin kallon da daddy kebina dashi kamar tsohon maye yasani kasa zama falon danhaka na lallaba nashige bedroom din hajiyar nai kwanciyata,Dantace mungama zama wancan gidan harsai megidan yadawo hayyacinshi tukunna.

Tashin Danai Sam beji dadinshiba duk da cewa yafarasamun nutsuwa adan yinin dayayi yau dinnan,Gashi yana kallo hajiya saita tofe kome da addua indai bashi zatai,Tanayi tana sababi.

Bayan sallar isha'I Saiga alhaji yusuf dawani malami Wanda takanas hajiyar tasa azomata dashi,Bansan da zuwanshiba Saida hajiyar taje ta kirani wai nima a kwankwasheni ko abin yashafeni,Saidai ni qalau nake daddyn nedai me matsala.

"Ai hajiya kamar dai yadda Allah ya bayyanamin to gaskiya sihirine kuma Allah ya takaita dan gabadaya da niyyar juya kanshi akayishi to Amma komai yazo da sauki danhaka saimudage da addua Allah yasa iyakar wahalar kenan Allah kuma ya kiyaye gaba,Yanzu abinda yakamata anan shine ga wannan rubutun nan ayoyine na karya sihiri da akai tofinsu cikin zamzam danhaka zaidinga shane yana shafawa Cikin hukunci na lillahi komai zai warware cikin kankanin lokaci indai yayi yanda yadace.

Godiya sukaimishi sosai tare ddabashi sadaka Sannan suka rakashi,Sai falon ya kasance dagani Sai daddy dake zaune yai shiru da alama wani tunanin yafada.

Kauda kaina nayi ga barin kallonshi ganin zai kallo inda nake.

"Jiddana" Sautin muryar daddy ta bugi kunnena yana kiran sunana,Acikin zuciyata na amsa kiran haka ko kallon inda yake banyiba,Amma kobabu komai nasami nutsuwar zuciyata tunda naji inda matsalar take.

Nasan haka kawai bazaimin abinda yaiminba,Ga tausayin zahra dake zuciyata Dan tunda taji labarin komai take kuka tare da furta inyi hakuri itace tajamin.

Jin yakuma kirana yasani mikewa tsam na barmishi falon,Lokacin Hajiya kaka tashigo falon daga rakiyar malam din.

"Kaga ai bazama zakaiba auta tashi zakai kayi sallar isha'i Saikasha wannan rubutun ka shafa inkuma baka iyawa saina shafamaka.

Da sauri ya dago kanshi yana kallonta jin wait m zata shafamai.

Harara ta wurgamishi kaini daina kallona da wa innan manyan idanun naka,Kana mamakine kocemaka akai bazan iyaba? To ko daya dan lokacinda na tubeka naimaka zirr na shafeka me nawama beganiba danhaka tashi maza ai ba zama zamuyiba dannatabbata zuwa gobe ahaidaniyar zatafara wani sabon aikin tunda yaudai batasami yanda takesoba.

''''''''

Sanye da farar jallabiya yafito me gajeran hannu sai tashin k'amshi yakeyi,Zama yai tare da

shafar kanshi"Nagama shafawa hajiyata.

"To Allah yaimuku albarka yakuma bamu dacewa Dan Allah kadage kaji?

"To Hajiya ins ha Allah zanyi yanda kikace,Amma ni Ina mzankwana?

"Yo inafa zaka kwana KOnan falo ai saikai kwanciyarka inkuma bakason nan din baga dakuna nan da yawaba saika zabi inda kakeso.

"Amma hajiya nida zahra ko?

"Taimaka ubanmi halan yarinyar dake fama da kanta, Kumama yanzu kasan da ita?

"Dan Allah kiyi hakuri Allah sonakeyi inbata hakuri.

"To indai hakane kajira zuwa safe saikabata.

Yamutsa fuska yayi tare dayin kalar tausayi tabbas akwai damuwa wlh Indai yau beji dumin matarshiba.
[5/9, 10:12 PM] Maman Dije: 59

Saida ya tabbatar da kowa na gidan yai barci Sannan ya lallaba cikin d'akinda nake kwance domin wata irin masifaffar sha'awa ke damunshi saikace yai shekara rabonshi da mace.

Sakin labulen tayi bayan taga shigarshi cikin d'akin dama tana sane tace jiddan ta kwana ita kadai, murmushi tasaki kamin tace habibu kenan Allah ya warware damuwarku cikin gaggawa ya tsarekai da sauran 'yan uwanka,Cikin wannan zamani me matukar ban tsoro.
Hajiya kaka kenan mace jajurtatta akan iyalinta.

Ajiyar zuciya ya sauke lokacinda ya rufe kofar bayan yashige dakin,Lallabawa yayi zuwa gadon kallo daya yaimin yaji yana kikarin idasa rudewa Dan wata farar rigar barcine jikina da hajiyar tabani kuma kwance nake cikin haske abuna, Dan bansan lokacinda barci ya daukeniba.

Rigarshi ya tube tare da lallabawa gefena ya kwanta,Harwani bugu zuciyarshi keyi Sabida tunanin yanda Zan karbeshi cikin wannan dare,Yo dama yaya lafiyar kura.

Ahankali naji saukar hannunshi cikin jikina bansan lokacinda na sauke ajiyar zuciyaba,Sabida akwai wani irin Sanyi a hannunshi,Afusace nai niyyar tashi Amma ya Hana hakan dan da karfinshi ya maidani cikin jikinshi yana sunsunar wuyana tare da birkitani da

zazzafan soyayyarshi.

Tun ina mutsu mutsun tureshi tare dason kwatar kaina harna gaji na daina Dan sosai ya shiryama hakan dama.
Kadan ya hanani inyi dariya jin yanda yake sakin sambatu da nishe nishe irin arude yake dinnan.

Yi yai kamar bazai barniba Dan saida nafara kuka Sannan ya sararamin.

Bayan komai ya kammala ina rungume ajikinshi Ina aikin kuka,Yayinda shikuma yai shiru yana saurarena tunanin ta inda zaifara lallashina yakeyi.

Saida yaga lallaidai ba shiru zanyiba tsawon lokaci Sannan yafara jijjigani da furta"Dan Allah kiyi hakuri kiyi shiru Jidda nagamafa kuma bazan k'araba shikenan ai ko banso kanki yayi ciwo kinji ko?

"Kan nawa yai ciwon ina ruwanka dani,Kuma sainagayama hajiya ince fyade kaimin.

Manyan idanunshi ya fiddo waje gabadaya daya kamin yace yi hakuri dan Allah na tuba matata bazan kumaba ki rufamin asiri ko so kikeyi hajiyan ta bugeni?

Tsakanina da Allah nadagamishi kaina Alamar eh dan har lokacin bandainajin haushin abinda yaiminba Amma dayake beda ta ido yanzu yawani lallabo ya tausheni"Nikatashi kabani waje tunda ka daina sona gobema gidanmu zanje kuma bazankumadawowaba bazan zauna dakaiba.

"Dan Allah yi hakuri Jidda bazan kumaba,Wallahi inasonki kema kinsani kece cikon farincikina Lallai idan babuke farincikina bazaitaba cikaba,Sannan bansan abinda yahau kainaba har hakan ta faru kinga yaranama duk fushi sukeyi dani kiyi hakuri kuma kitayani shawo kansu,Nasan ma indai kika hakura suma zasu hakura bazan kumaba kinji.
Kuma shigar da hancinshi yayi cikin jikina yana furta"Nai kewarki sosai Jidda duk dare bana iya barci,Jikinki yakuma canzawa indan k'ara kadan? Ahankali zanyi kinji matar albarka!!!

K'okarin kwace jikina nakeyi amma ya rikeni kam yana murmushi,Ganin danayi da gaske yake yasani furta " to kaje kayo tsarki"
Dariya yasaki ahankali yanakuma shigewa jikina,"Karki damu yau basainayiba idan nagama zanyi tsarkin gabadaya.

Duk tirje-tirjena be hanashi kumayiba sosai jikina yai ligif sabida wahala.

Ina rungume jikinshi har Saida barci ya kwasheni Sannan ya lallaba yatashi fuskarshi cike da

walwala,Wata irin nutsuwa dayarasa cikin kwanakinnan yajita yanzu tana sauka jikinshi, Alhamdulillah yake nanatawa cikin zuciyarshi da fili.

Gudun fitinar da zan iya gwadamishi yasashi barina nai barcin sosai inyaso idan ya farka sai ya tasheni na gyara jikina.

""""

Da ciwon jiki natashi ga tashin zuciya kamar ankarominshi haka kawaima yunkurin aman nakeyi.

Adaddafe nai sallar asuba bayan yadawo Dani daga wankan da kusan shine yaimin shima.

Ki daure inkawomiki ko tea ne inaga kamar hadda yunwa Jidda bakison cin abinci.

" Bawani nan bakaine jiya kakusa kasheniba kumama ai banso kaimin dole ko!!!

Bakinshi yadafe kamin yace"Naji autar Mata laifinane naimiki dole Amma kuma ai kin temakeni kuma nagode sosai tunjiya nake shimiki albarka nasan kinsami lada me tarin yawa,Inje inkawo miki tea din?

[5/24, 4:23 PM] Maman Dije: 60

Idanuna kamar zasu fado haka nake harararshi Amma bawan Allah ko ajikinshi hasalima saikuma lallashina yakeyi.

Da kanshi ya shiga kitchen,Dan har hajiyar ta tambayar"Kai waye nan?

Kanshi AK'asa ya furta nine hajiya tea Zan hadama jidda.

Wuceshi tai tana murmushi"Shakiyyin wofi yanaso yana kaiwa kasuwa.

Kusan da daru yasamu nasha tea din kuma saigashi naji dadin jikina Dan dama hadda yunwar.

Sai nan nan yakeyi dani nikuma saiwani basar dashi nakeyi Dan tuni na huce tunda ba laifinshi bane Allah ne ya jarabcemu ta hakan,Sannan koba komai namiji beson mace me riko sunfison dasun baki hakuri to ki hakura.

Ina kwance da safe shikuma yanacan gefe zaune,Yaran sukai sallama suka shigo duk gaidani sukai tare da min sannu da jiki,Sai suka kama kallon uban batare da sunyimishi maganaba.

Ina cikin bargon na kalli Sadiq "Kai Sadiq bakuga daddy bane kuma haddakai babba?

Duk gaidashi sukai tare da ficewa suna turo baki musamman Sadiq Dan shine babba kuma yafisu hankali.

Kallona yayi tare da furta" Jidda kinga yanda yara sukai fishi dani ko? Abunda betaba shiga tsakanina dasuba Dan Allah kisaki jikinki dani nasan suma zasu saki,Amma kina dauremin ko nuna rashin walwala zasucigaba da zarginane akan Ina cutamiki.

Cusa kaina nayi cikin bargon batare dana kulashiba,Amma duk dahaka nai niyyar yima yaran magana dankada abun yai nisa.

***

"Kinga aikin danaimiki ba kalar wanda nasaba yima kowabane shiyasa na amshi kudinki da yawa, Amma dama ai saidanagayamiki Akwai Matsala fa to ai wannan shine matsalar mahaifiyarshi tsaye take kyam akanshi yanzu haka idan kika matsa akumamishi wani abu to duk abinda akai kanki zai dawo maganar gaskiya inkuma kinaganin ayi wani to? Bama wannan ba mezaihana kije ki hada da 'yan dibarunku na mata ko hankalinshi zai karkato zuwa gareki ko?

Kwallar data cikamata ido ta goge tare da kallonshi ka barshi kawai bari inje Amma Zan dawo kome kenan saimuyi magana.

Wani k'aramin tsaki yaja bayan barinta bukkar tashi,  wawuya kawai asararra,Mata halinku saiku ko wacce mace sai shegen son kan tsiya Sam wasu basu da tunani mata da yawa na mantawa da wannan kalmar ta k'addara tabbas duk Wanda yayi hakuri to hakika kaddararshi zata sameshi walau me dadi ko akasin hakan.Idan namiji ya kasance akwai aure tsakaninku tofa basaikin bi malami ko boka ba zakisame ba A a addua kawai zata jawoshi gareki,Amma Ina amfani ajawo soyayya da tsiya sai ya aurekin sati daya yai yawa anfara fada daga karshe yafara ganin bakinki sai maganar saki to dama badan Allah akayiba,Wani tsakin yakuma ja kamin yace kodayake inda babu gafalallu kamarku aida bamusami kudi ba.

Note.

Dan Allah Mata mu kula da halin rayuwa nayau da kullun tabbas duk kusan kura-kurai na duniya Mata ke aikatashi yau Allah ya kawomu wani zamani da babu wani aiki na laifi da Mata

basu aikatawa,Wai ina rauni da tausayi wanda Allah ya haliccemu dashi? Amsar itace babu sabida munyi watsi daduk kusan damar DA Allah yabamu.
Mutuna ayau idan Allah yasa mijinki zai auri mace goma wallahi kuna tare zai aurosu kuma duk Wuya kuna tare Amma idan mukai hakuri saimuga komai yazomana da sauki,Tabbas hakuri nada wahala amma yinshi kawai shine mafita agaremu.
Allah kasa mugane ka shiryar damu hanya ta daidai.

""""""""

"Am Jidda nace ba kidan tambayarmana hajiya mana mukoma gida wallahi nagaji dazama waje dayannan nasan kema zakifi sakewa idan muna gidanmu,Naimiki Alkawari babu inda zanje kinji?

Kallo daya naimishi na kauda kaina,Batare dana tankaba dan gaskiya inajin tsoron mukomacan kuma yadasa daga inda ya tsaya,Dannasan sihiri becika warwarewaba gabadayaba kuma lokaci daya,Nasandai dole sai anbi komai sannu.

Kwanciya yayi kusa dani tare dadan sunbatar goshina yai lamo ya na shakar kamshina yayinda nima nakuma shigewa jikinshi dan sosai turareshi kekuma shigardani.
"Bazaki kulaniba jidda? Shikenan kidai k'ara hakuri bazan kumaba insha Allah.

***

"Wai zahra ni amatsayina na mahaifinki Amma ki shareni tsawon kwanakinnan kinaganin kin kyauta kenan?

Turo bakinta gaba tayi kamin tace"To daddy aikaima batamu kakeba ko?
"Zan bata rankifa zahra kome nayi kuma saiku biyemin bazaku tayani da addua ba ko cemiki akai dole kullun mutun saiya kasance akan daidai? Kumama ai ba halina bane yakamata kuyimin uzuri ita wadda naima laifinma ta hakura Amma ku kunkasa mantawa inace yanzu nadawo lafiya ko? Yanzu idan aure nace zan k'ara wannan wulakancin zakuyimin?

Da sauri ta kalleshi"Aure kuma daddy?

"Eh mana ko cewa akai dole da ita kadai Zan zauna?

"Tab Allah daddy saidai ka saketa nima asakoni indawo gida Amma babu matar da zata

zauna gidannan ta cutarmin da k'anne,Wai kamasan irin YARDAR dake tsakanina da aunty din dahar na yarda ta zamo makwafin mahaifiyarmu? To wallahi ko iyayenta bazasu yardaba haka yayanta surukin naka na tabbata duk irin son da yakemin saiya sakoni domin basu hada sonta da komaiba,Kasanko wannan abun dayafaru ko barcin kirki dainawa yayi? Kai meyasa bazakaji tausayintaba amatsayinta na marainiyaba gaba da baya?

Ajiyar zuciya ya sauke "Lallai yarannan sun dauramana wani ta kumkumi da Allah,To shidai dama beda ra'ayin rike Mata biyu tunda yake,Sannan bazaiyi fatan wani Abu Mara dadi yashiga tsakaninsuba danhaka dole ya kiyaye komai da iznin Allah.

Ganin ya zubamata ido Amma yai nisa cikin tunani yasata mikewa tabar d'akin.

"Aunty har yanzu jikin yaki dadi ko?

"Wallahi kuwa zahra narasa abinda ke damuna gashi gobe zamu koma makaranta ni bammasan yanda zanyiba jiyama da dare saida daddy yasamin drip.

"Allah ya sawake Amma gaskiya kinyi saurin yima daddy hakuri yakamata ace kin nunamishi bacin ranki sosai danya kiyaye gaba Amma sainaga saiwani kulashi kikeyi namiji ne fa?
[5/24, 4:23 PM] Maman Dije: 61

Haba zahra yakamata fa ki tuna daddy ne babbane shi kuma yasan abinda yakeyi yakamata mudinga yimishi uzuri shi ma beji dadin abinda yayiba,Babu komai awajena ya wuce Kawai saidai mutari gaba kuma.

"Humm wani lokacin haushi kikebani wallahi, Daddy mahaifinane bazanso abinda zai sakashi cikin damuwaba Amma abinda yayi yakamata ace kin tauna tsakuwa Dan aya taji tsoro,Amma kinwani biyemishi kilama har kanki saida kikabashi ko?

Murmushi kawai nayi tare da kauda Kai na "humm zahra kenan nima ai na dauki mataki yanzudai ba wannan ba Dan Allah kiyimin tuwo yanzu ko kadanne wallahi haka kawai nake sha'awarshi.

Ajiye hijab dinta tayi tare da mikewa to shikenan bari inje Amma Dan Allah kidaina sakarmishi fuska har sai yagane kurenshi nasan lokacinne zai San kinada Rana wajanshi nifa raina yabaci sosai wallahi.

""

Duk zaune muke afalon Hajiya kaka yau kwananmu uku agidan sai yau taga damar barinmu mukoma namu gidan,Fada da sababi gami da mita babu kalar Wanda batayimishiba daga karshe dai saida taga lallai yashiga taitayinshi Sannan tace kutashi kuje amma duk abinda kaga tana bukata to ka kira ayimata nan Saura idan ankwana biyu ka dinga barci babu addua kajika zakaga yanda Zan sauyamaka kamanni.

Sadiq ne ya guntse bakinshi sabida dariya,Yo ai abinne yanzu yaya Hajiya zatayi da daddy koda akwance yake balle wwai zata canzamishi kamanni.

***

Hankalinshi na kaina duk da tukin mota yakeyi,Nikuwa nai lamo cikin kujerar hankalinama ba kanshi yakeba.

"Jidda ko zamu biya asbt ne akuma dubaki?

.

Manyan idanuna na lumshe "a a karka damu inajin sauki tashin zuciyarne ke damuna.

"Sorry zaki warware insha Allah bari mubi ta cikin gari ko zakiga abinda kikeso Amma Dan Allah kisaki jikinki kinji?

Nidai kwantar da kaina kawai nayi Dan Sam wani lokacin ko magana banso wlh.

***

Malam kamar yadda naimaka bayani sonakeyi ya aureni kuma idan ya aurenin to in mallakeshi sai abinda nace ko mahaifiyarshi sainace Sannan yaimata.

"Subhanillahi baiwar Allah meyai zafi haka duk meyakawo wannan zancen amatsayinki na musulma? To maganar gaskiya ni ba kalar wa innan bokayen bane dake fakewa da malunta suna aikata fasadi akan kasaba,Kuma kullun adduata anan shine Allah yakareni daga fadawa wannan halakar!!!Maganar gaskiya lokuta da dama ku Mata kuna aikata kuskure musamman idan maganar soyayya tashigo ciki, Duk abinda baka da rabo akanshi to tabbas bazai zama nakaba idankuma ka kwaceshi da tsiya to tabbas saiya kufcemaka danhaka tunfarko gara ka nemi zabin Allah yabaka mafi alkhairi,Wannan maganar wautace ba k'aramaba amatsayinki na musulma wadda ta yadda da k'addara me kyau ko akasinta tabbas akwai matsala da damuwa

akan abinda kakeso ka rasashi ko baka sameshiba Amma sai Inga babu wata mafita datawuce hakuri DA Addua idan Ayau jikai asiri Wanda kika aureshi to kisanifa dole saiya sakeki domin abun zai iya sakinshi koda yaushe kuma saiyaji babu dadin zama dake,Danhaka garama Kiyi addua idan da Alkhairi Allah ya daidaitaku inkuma babu Allah ya kawomiki daidaike kuma mafi alkhairi Dan haka kudaina wannan kuskuren na siyen masifa da kudinku tunkamin lokaci ya kuremuku.

Kuma har kinada bakin da zakice ashiga tsakaninshi da mahaifiyarshi? Ke kuwa kinsan wacece mahaifiya? Ke yanzu Idan akaimiki haka zakiji dadi? Kokuma ayima mahaifiyarki haka zakiji dadi? Yaya zakiji idan kikai dakon cikin yaronki watanni Tara sannan kisha nakuda ki haifeshi kuma kidasa raino har ya girma yazama mutun lokacinda kike tunanin zakifarajin dadinshi kawai kuma saiwata mace Asama ta rabaki dashi yaya zakiji? Ina kuma matar zatakai hakki irin wannan?

Danhaka ki kula duk abinda bazakaso aimakaba to ko cikin zuciyarka kadda kai tunanin yimawani,Waima Ina maganar manzan Allah (s.a.w) inda yake gayamana cewa imanin dayanmu baya cika harsai munsoma 'yan uwanmu abinda mukesoma kammu kenan yanzu duk munada k'arancin imanin kenan ko?

Kuka takeyi sosai jikinta yayi Sanyi lallai tayi kuskure Amma ta tuba kuma bazata kuma aikata kuskure irin wannan ba.

Godiya taimishi me tarinyawa Sannan tabarshi.

To dama haka rayuwa take ai.

Yanda ka dauketa haka take zuwamaka domin Allah da kanshi yagayama baya dorama wata rai face sai abinda zata iya, Dan haka idan har kakai kanka mahakala to kaddama kace wai Allah ne ya jarabeka a a kada ka zargi kowa sai kanka.

[5/24, 4:23 PM] Maman Dije: 62

Bayan kwana biyu.

Jikifa kullun kuma laushi yakeyi kusan adaddafe nakezuwa makaranta sainayi kamar ma kar inje hakanan nake daurewa gudun matsala Dan gaskiya inason karatuna sosai.

Gashi abinci be ciwuwa ko ruwa nasha saiya dawo shiyasa sai inkicin komai shikuma yaita naci tokuma danacin saiya dawo, Nan da nan na fige na lalace fuska sai uban hanci da idanu,Gawani irin fari danayi kirjina ya ciko haka 'kuguna Amma daga basuba babu abinda keda auki ajikina.

Kuka nakeyi sosai hadda sheshsheka dan ciwon yajemin ko ina Neman mafita kawai nakeyi Toma wani irin ciwone wannan?

Inajin yaran cirko-cirko akaina amma Sam batasu nakeba nidai fatana insami saukin jikina.

Shigowar motar daddy yasasu nufarshi ko wanne da damuwa fuskarshi.

"Lafiya naganku haka sadiq?

"Daddy aunty ce keta kuka bata da lafiya kuma tunda muka dawo makaranta ko ruwa batasha ba yau.

Da sassarfa ya nufo dakina danhaka ahalin kukan ya taddani,Allah yasa Sadiq yai hankalin tsaresu falo,Dankuwa gabadaya arude ya rungumoni jikinshi ya na lallashi.
"Sorry Jidda yi hakuri nasan da wahala Amma daurewa zakiyi inshaAllah zakisami sauki me kikeso in siyomiki?

Banza nai dashi Ina kukana,saida naga ya gigice da tambaya Sannan na tsagaita da kukan"Daddy nagaji DA wannan ciwon Dan Allah kakaini asbt agwadani wallahi bantaba ciwo irin wannan ba ko mutuwa zanyi?

Maidani yayi cikin jikinshi yanajin babu dadi"Daina fadin haka Jidda babu abinda zai sameki sai Alkhairi babynmune ke wahal dake Amma zai daina kinji?
Kallonshi nayi ido cikin ido kamin ince baby daddy.

Dan shafa sajenshi yayi numfashinya na canzawa"Eh Jidda akwai ciki jikinki kuma duk muna buk'atarshi Dan haka kiyi hakuri ki haihu Dan Allah.

Ga mamakinshi saiyaga nakuma shigewa jikinshi Ina sauke ajiyar zuciyar kukan danasha,Sam beyi tunanin hakanba yai tunanin wata sabuwar rigimar ce,Tokuma gani yayi boyewar bata dawani amfani musamman dayake ganin irin wahalar danakeyi.

Shafar bayana yaitayi cikin wani yanayi danfa dama amatukar takure yake baby yahanashi rawar gaban hantsi.

Tun Ina tunanin shafar iyaka ta lallashice saigashi ya zarce Dan tuni yafara sakin layi.
Dakyar na kwaci kaina daddy cikin dakina mukefa yaran zasu iya shigowa kuma jikina babu Dadi!!!

"Yi hakuri Jidda nagaji wallahi amatukar takure nake Dan Allah kiyi hakuri ko kadanne Dan mitsima ya isheni.
Hannuna yakama zuwa d'akinshi duk da irin tirjewar da nakeyi, Dannasan muna shiga zai sauke gajiyarshi akaina duk da wannan rashin lafiyar tawa.
Saina tuna wata hira danaji Matan kannen Abbana sunayi.
Wai daga zarar shekarun namiji sunfara mikawa shikenan sai kuzarinshi ya ragu wanima bazai iya kula da buk'atar matarshiba,Amma abinda nakasa ganewa akan daddy shine duk lokacin zamu kwanta dashi sainaji jiki anya maganar gaskece kuwa? Kokuwadai Ana magana

ne akan maza wa inda basu kula da kansu? Irin wa inda Rana da zafi ga basir suka cinye,Dan gaskiya ban tunanin daddy yanada wata matsala.Tokuma kodai danni yarinyace awajanshi sosai?

Yankewa tunanina yayi lokacinda najini saman gadonshi.
Azabure na mike shikuma yakuma damkeni yanawani marairaicewa"Habamana Jidda wai sai yaushe za afara yin abinnan cikin dadin raine? Ki tausayaminba kumafa lallabaki nakeyi duk lokacinda Zan nemeki Amma saikin nuna bakiso kinaso incutune? Tunda ina ganinki kullun kuma inaso ke halaliyatace idan banzo garekiba Ina kikeso inje,Yanzu yaushe rabona dake Jidda tunfa agidan Hajiya kumacan dimma so daya kacal nayifa!!!

Cikin shagwaba nace"Toni daddy akwai zafi fa!

"A a jidda wallahi babu zafi saidai wahala da gajiya zakice amma ai yanzu babu zafi tunda inashiga jikinki Lafiya lau.

Turo bakina gaba nayi alamar dai baniso.

Jawoni cikin jikinshi yayi cikin sigar lallashi "To shikenan yi hakuri inyi d'an mitsi kuma ahankali idan naimiki mugunta zanbari ki Rama kinji?

Da wayau DA lallashi amatsayinshi na babba ya kwantar dani tare da rufeni da zazzafar soyayyarshi,Tuni nabada kai bori yahau.

Munaji ana kwankwasa kofar amma tsakanina dashi akarasa Wanda zai motsa balle abude kofar, Kuma tunda akanace kwankwasawa to abune me muhimmanci.

Muryarshi ashake kamar Wanda aka tada barci ya furta waye?

"Daddy nine baba kamal ne yace inkawomaka wayar"

Shaf ya manta da sunyi zaizo gidan yaduba Jidda idan yadawo aiki.

"Je ka budemishi get Sadiq kace yashigo na manta megadi benan.

" Jidda tashi muje in wankemiki jikinki ga kamal nan zai dubaki.

Yamutse fuska nayi batare Dana kalleshiba danni nagaji.

Wucewa yayi ya gyara jikinshi Sannan yazo yaigaba dani dan ko magana beminba,Saidai najini cikin ruwa.

Da kanshi yaimin wanka Sannan ya nadoni soyai in shirya da kaina amma ganin ina niyyar kwanciya yasashi sakin dariya Lallai aiki yasami manyan mata,Allah hadda yunwa ke damunki Jidda shiyasa jikinki Sam babu karfi, Dago hannun insakamiki rigar nan muje kamal ya dubaki inma asbt zamukoma sai mukoma din nafiso inji jikinki da kwari.

Saida ya kwantar dani falo Sannan yafice waje Dan kamal din kin shigowa yayi yanajiran iso tukunna.

***

"Kai mutumin inanan tsaye ina jira nace badai Mara lafiyar ka tausheba inata kiran wayarka saidai yarona ya dauka"

Hannu ya mikamishi suka cabe kamin ya dora"To sarkin sharri nibabu abinda nayi.

"Karya kakeyi wallahi wannan lemar ruwan na uban maye kace kawai kaine ke kuma kwantar musu da yarinya.

"Dan Allah kabar fadi muje ka dubata ko jiya saida nasamata ruwa Sam batason cin abinci [5/24, 4:23 PM] Maman Dije: 63.

Idanuna alumshe suka shigo dakyar na samu natashi zaune tare da gaidashi.

Amsawa yayi asake yanayimin Sannu.

Kallon daddy yayi, Inaga saitasha ruwa da yawafa Dan asami kwarin jikin kuma dole saika kula da abinda zata iyaci kaga saikaita kokarin samomata yunwace kawai taima jikinta illa,Kaban mamaki Allah saikace ba likitaba!!

"Bazaka ganeba kamal Allah ina dubata jikinne Sai inga kamar kullun kuma saki yakeyi ma shiyasa nace bari inyimaka magana.

"Babu komai yanzu kasamo wa innan afara saimuga abinda za ai dagabaya,Yai maganar yanacigaba da rubutun da yakeyi,Mikamishi takardar yai"Gashi yi sauri Dan Allah hajiyarmu ke jirana wlh.

""""

Cikin barcin dayafara dibana naji shigar allura sonai in zabura amma naji nakasa Ashe rikeni yayi sosai tunda yasan bawani son allura nakeba.

Lamo nayi ajikinshi har aka gama samin sannan ya kwantar Dani yatafi rakashi.

Sannu aunty gaskiya babyn nan nabaki wahala wallahi harna farajin haushin babyn,Cewar Sadiq cikin damuwa.
Dan murmushi nayi tare da shafar cikina Wanda yake alafe kamar ma babu hanji cikinshi tsabar yanda yake lafe.
"Yaya Sadiq Ina babyn take? Cewar Mimi.
"Auntyce zata haifomana idan tasami sauki kimata addua ta warware kinji!

.

***
"Baban zahra yakamata kafa dagamata k'afa har tasami nutsuwa gaskiya kagadai jikinnata yanda yake ko?

"Wallahi bawani takurata nakeba,Yauma kasa hakuri nayi dan rabona da ita anfi sati biyu sabida wannan matsalar da mukasamu sai gidan Hajiya shima dakyar ta yarda to yaukuma naji nagaji ainayi kokari.

"Eh hakane kam danni ko kwana biyu ban iyawa ko fashin sallah take saitamin 'yan dubaru,Bari inje samatashi kawai zakaitayi daganan har zuwa dare nasan idan sunshige jikinta zataji dama dama Allah yabata lafiya ya kawomana wannan baby Lafiya.

Barci nakeso inyi amma sunkacame hirar baby,Saida yashigo Sannan suka fice, Faruq na fadin yanzu gidan duk babu dadi sabida rashin lafiyarki aunty Dan Allah kiyi ki warke.

Da kallo yabi bayansu yana sakin ajiyar zuciya,Kamin ya raba gefena ya kwanta, Sai tunanin mahaifiyarsu ya fadomishi arai gaf da zata rasu kusan kullun saisunyi rikici da ita sabida matsamishi da takeyi akan yakamata yai aure Dan yaran su saba da wata badole sai itakadai mahaifiyarsuba,Shikuma alokacin abinda kebashi haushi kenan takawo maganar mutuwa Ashe Ashe lokacintane take hangowa.

"Haba Abban zahra nifa sai Inga kamar ma yanzu ka daina sona shikenan kai daga magana saika kama fada kumadai ai maganata gaskiyace kowa zai mutu bawai ni kadaiba kuma kasani danhaka dole ingayamaka gaskiya ni mutuwa zanyi nan kusa inma zaka shirya shirya,Maganar marigayiyar keyimishi kuwwa adaidai wannan lokacin.
Matsawa yayi jikina yanajin yanda zuciyarshi ke tsananta bugawa,Kamar alokacin takemishi

maganar.
Rungumeni yayi jikinshi cikin Sanyin murya ya furta"Kadda ki barni Jidda Dan Allah mu kasance tare inafatan Allah ya dawwamar damu cikin farinciki nagode da kikasance cikon farincikina Allah yabani ikon farantamiki yarabaki da abinda ke cikinki lafiya.

Ahankali na Dora hannuna saman fuskarshi"Ameen daddynmu Allah yabarmu tare.

Matseni yayi jikinshi cikin farincikin jin amsar dayasamu,Wani Dan karamin Kara nasaki jin yanda ya matseni jikinshi,Da sauri ya sassauta rikon da yaimin tare da furta"Sorry, Kina bukatar wani abune inkawomiki?

Cikin shagwaba na girgizamishi kaina,Idanuna arufe dan barci nakeji.

""**""

"Zee na hakura da Dr.Habib wlh Dan saura kadan infada cikin halakar datafi wacce nakeciki,Ke wannan malamin fa cewa yayi sainakawo wasu abubuwa na jikin shi Dr.din naga Ina zansamesu dole na hakura waikuma naje wajan wani wai saiya aljanu sun kwanta dani sau bakwai kumafa karya sukeyi sune ke kwanciya da mutun saisu fake da wai aljanu haka kawai inje a sakamin cutar kanjamau Ina zaman zamana.

"Humm ai shiyasa kikaga naja baya wallahi, Ni wa innan karerayinne banso na malaman tsubbun nan Amma sai kukeganin kamar nacika son kudi, Wallahi duk mayaudarane yanzu kiduba kiga yanda naso Nasir kamar Zan mutu Amma ya dinga wulakantani yana tozartani saigashi danai hakuri kuma na tattarashi na watsar bagashiba yanzu shine me bina kamar zai haukaba,Insha Allah karshen watannan ma zankai maganarshi gida muyi aurenmu lokacin nagama jamishi rai,Danhaka wallahi tun wuri ki Kama kanki ga mazanan da yawa ciki bazaki rasa na aureba tundadai yanzu auren kk so.

Dama haka rayuwar duniya take me cike da qalubale Saidai kai fatan tazomaka da sauki.
[5/24, 4:23 PM] Maman Dije: 64

Bayan sati daya.
Shigowarmu kenan daga makaranta wanka kawai mukayi,Nafito Dan Dora girki sukuma yaran gyaran Gida duk da haka hira mukeyi tsakaninmu duk da cewa kowa da abinda yake.
Naji saukin jikina Sosai tsaknin jiya da yau, shiyasa harnasami sukunin danyin walwala.

Daddy ne ya maidomu gida, Do min yanzu tunda nasami cikinnan shike kaimu kuma shike maidomu,Amma yau ko shigowa gidan beyiba yana diremu ya koma da alama aiki gareshi.

Tuwon shinkafa naimana miyar ganye wadda ta wadatu da naman sa tuni gidan yagama budewa da kamshi,Yaushe rabon danayi girki dole na daddy mukeci,Dan ya hana a amso nawani gidan.

Saida nahada lemon kwakwa Wanda yake mahadin tuwon Sannan nashiga wanka lokacin har anfara kiran sallar magriba.
Wanka mekyau nayi sabida inji dadin jikina Dan rabona dako wankan kirki nakwana biyu,Amma yau jikin da sauki sosai Dan babu inda keyimin ciwo.

Saida nai Sallar magriba sannan nakoma gefen gado na zauna ina shafa,Shafarma kanta yau ta dabance,Kai inama haka zanta samun sauki kullun aidanaji dadi.

Tare dasu Sadiq daddy yashigo sabida sunfita sallar isha'i.
Sannu da zuwa naimishi kamin nacigaba da jera abincin,Wani irin kallon sha'awa yabini dashi,Dan yaushe rabon da ya ganni cikin Lafiya haka,Ga wani irin kyau da jikina yayi,Danshi aganinma saiyaga kamar yanzu nafara girma.

Inata magana ganin bejiba yai nisa cikin tunani,Yasani dan zungurinshi kadan.

Lumshe idanunshi yayi kamin ya budesu akaina.
"Cewa nai ga ruwan wankan can"

"Ok to Jidda bari nadankuma hutawa kadan nagaji da yawa ne yau gakuma yunwa inaji,Rabona da wani Abu tun tea din safe.

"Subhanillahi to ko abincin zanfara kawomaka?

Riko hannuna yayi ya zaunar dani gefenshi Saiwani mayen kallo yakebina dashi"Share kawai jiddana zanfara hutawa tukunna daganan sai kimin wanka Saikuma inhuta saimuci abincin inafatan hakan yayi ko?

Kauda kaina nayi inadan murmushi ganin yanda yai maganar k'asa-k'asa duk da cewa yaran kallo sukeyi Amma haka yake yana matukar yin takatsantsan wajan ganin basuga wani Abu na ashsha daga gareshiba.

"Kinyi kyau jiddana yaushe rabon danaganki cikin walwala haka? Inafatan zaki bani

hakkina yau ko?

Dan ja baya nai kadan kamin ince"Kai daddy Dan Allah daga samun saukina? Inkuma kakuma jawo ciwon fa?

"Habamana jidda zokiji Allah ahankali zanyi kuma kadan kinga nakwana biyu babu wani bayani sabida yanayin jikinki ko kinaso sha'awa ta cutar dani ne?

Yamutsa fuska nayi amma ban kalleshiba,Dan daddy Sam babu wasa mutunne me karfin jiki da kuzari zai gama lallabanine yanzu amma danashiga hannunshi nagama yawo.

Tashi yai tsaye "muje ki hadamin ruwan wankan sai inhuta gabadaya ko!!!

Inagaba yana bayana har cikin bedroom dinshi,Ina kokarin hadamishi ruwan saigashi yashigo, mikewa tsaye nai Ina kallonshi yayinda shi ma ya zubamin manyan idanunshi wa inda sukadan surka yanzu zuwa launin ja.

"Pls jiddana ko kadanne kinji?

Tausayi yabani ganin yanda yaiwani iri dashi da alamadai amatukar bukacen yake"Eh na yadda daddy amma ba yanzuba nidai sai zamuyi barci.
"To shikenan hakanma yayi nagode sosai Allah yaimiki albarka lafiyar jikinki ta dore.

Samunai nafice ina dariya,Jin yanda yaketa sambatunshi shi kadai.

""""""

Yaga nazo yaga nazo Amma shiru dole yatashi yasaka jallabiyarshi ya nufi kofa yanajin hakurinshi nakuma k'arewa.
Turus yaja ya tsaya ganinmu gabadaya afalo duk k'arin karatu naimusu Wanda munkwana biyu bamuyiba sabida jikina,Saikuma Mimi me wasa.

"Ah ashe baku kwantaba?

"Eh daddy karatun aunty ta doramana sabida ankwana biyu bamuyiba,Cewar Sadiq.

"To Masha Allah Allah yabada lada,Oya azo akwanta akwai makaranta gobe kadda Ku makara fa!

Araina nafurta kunjishi kawaidai yakosa inje yakusa kasheni zaiwani Kora yara,Amma

azahiri ko kulawa da zancen banyiba saima littattafan danake hadewa waje guda.

"Oh Jidda wai sokikeyi saina digene wajan nemanki Dan Allah kitaho hakanan!!!

"Kai daddy to bazan shafa mai ba?

"A a zaki shafa baby na kawoma in tayaki shafawa.

Tun kusan cikin dakina mukafara sakin layi kamin daddyn yai karfin halin jana zuwa dakinshi Wanda yakuma gyareshj Sannan yaketa tashin wani sassanyan kamshi, me matukar dadi da kwantar da hankali.

Bewani tsaya sanyaba yafara koyar dani karatun kauna Wanda nima banwani tsaya jan ajiba nafara daukar darasin nashi tare da kokarin biyawa.
[5/24, 4:23 PM] Maman Dije: 65

Sai juyi nakeyi Amma nakasa tashi tsabar yanda jikina yagamayin laushi,Shiko ai barcin jin dadine yaigaba dashi.

Ahankali natashi zaune jin marata tawani kulle waje daya kamar irin zanyi period dinnan,Kuma cije libs dina nayi kamin nakai hannuna jikinshi"Daddy daddy tashi Marata"

Ganinshi kawai nayi azaune ya na murzar idanu amma da harwani munshari yake fitarwa"Jidda me kikace?

"Daddy marata ta daure sosai kamar jini zai Zubo.

"Ah subhanillahi Sannu jira ina zuwa kwanta kadda kiyi wani babban motsi kinji? Yauwa jiddanta kiyi lamo bari inzo.

Da sauri yadaura tawul akugunshi yatashi Dan harwani rawa jikinshi keyi, Tundanaga yanufi akwatin karikitan kayan aikinshi na yamutse fuska Dan inbawani Iko na Allah ba zai Iya cewa zaimin allura ilaikuwa kamin ingama tunanina naga ya na daga allura ya na dubawa da Alama akwai wacce yake nema.

Baki na tabe ganin ya nufoni da allura niko,Dan murmushi yayi kamin yace"Yauwa babyna

Allah yaimiki albarka ya barmu tare,Taho in rungumeki cikin kirjina sannan inyimiki allura Amma bame zafiba insha Allah.

"Nidai gaskiya a a wallahi banso.

"Ah rufamin asiri jiddana kinaso in yi asarar gudan jininane? Juyamana ahankali zanyimiki kinji!!!

Da lallashi daban baki yasamu natsaya yaimin alluarar Sannan yaimin wanka da kanshikuma har lokacin bebar lallashinaba sannan ga sannu dayaketa furtamin saikace wadda kewata jinya.

***

Da asuba yana dawowa masallaci yacika DA dadin baki akan lallai inyi hakuri yadan k'ara Dan mitsi Sabida yanaso baby yasaba da abin.

Nidai DA wuri nace ban yardaba Amma ahakan saidayayi,Kumafa karkuyi zaton wai banajin dadi A a ko daya inajin dadin abuna kawaidai nafison in nuna banso Dan inga yanda yake marairacewar ne.

Tunda garin Allah ya waye yake shawagi tsakanin dakinshi da falo zuwa kitchen Amma shiru bantashiba ga yaran nata kallon agogo suna tambayarshi,Daddy zafamu makara.

"To auntynku taki tashi kumadai kunsan bazan tashetaba tunda bawata lafiyace da itaba,Yautasami barci bekamata atashetaba yanzu,Inaga yanda za ayi kawai ku karya sainaje na kaiku zanga malamin nasu.

Dole yatafi kaisu Dan kadda murasa muduka.

Da zahra yafaracin karo tsaye harabar makarantar da alama dama su takejira.
Gaidashi tayi kamin ta Dora da tambayar "Daddy ina aunty fa?

" Dan shafar kanshi yayi kamin yace yau tayi nauyin barci har muka fito bata tashiba to kinga sabida yanayin jikin shiyasa saina kyaleta,Amma yanzu zanga Wanda yakamata akan matsalar sabida dama yanzu dole zata dinga fashin makarantar sabida jikin,Kekuma saikiyi kokarin rinka bawasu Sadiq aikin DA akayi su kaimata duk ranar da kikaga batazoba,Muje ki rakani wajan principal din naimishi bayani.

Bewani sami matsalaba tunda maganace ta kudi sannan ga furucin aure dayashiga ciki,Dan shi dakanshi yace zaisa adinga ajemin dukkan wani Abu daya gudana Randa banzoba.

***

Cikin iko na Allah sai wajan 11 nasafe natashi,Kuma cikin kuzari da walwala.
Akunyace na rufe idanuna ganin yanda muka hada ido DA daddy Wanda keta kallona kamar zai cinyeni.

Murmushi yasaki kamin ya riko hannuwana"Oyoyo jiddan Habib barka da tashi.

Cusa kaina cikin kirjinshi nayi Ina murmushi.
Mikar dani tsaye yayi yana dariya"Kai gaskiya Habib be kyautaba yau ya hana amaryarshi zuwa makaranta ko!muje naimiki wanka saikici abinci in kaiki makarantar yanzu.

"Ah daddy ni bazanjeba ai dukana zasuyi yanzu Rana tayi.

"Kashh daina fadi waye ya isa ya bugi matar Habib Al babushi naje makarantar dazu kuma naimusu bayani danhaka kadda ki damu Indai Zaki iya zuwa to babu matsala inkuma hutun kikeso to saimu Bari sai gobe kinga nima yau ko aiki banjeba sabida Ina tunanin yanda zaki tashi,Ammadai marar ta daina ciwo ko?

"eh babu inda kemin ciwo saidai yunwa kawai sanakeji"

"OK to muje in cudaki sarauniyar mata.

""""***"""""

Duk wata irin kulawa DA kuka sani Ina samunta sosai, Hankalina ya kwanta dan gabadaya hankalin daddy na kaina hajiyata da hajiya kaka har kasa banbance Wanda yafijidani nakeyi sakaninsu,Haka su faruk sosai sukeson cikin dake jikina duk da cewa haryanzu be fitoba kumawai yashiga wata na uku yanzu.
Kowane gidan aure bazaka rabashi da matsalaloliba wasu da yawa wasu qalilan tonidai gaskiya Zan iyacewa matsalata bata wuce ta yawan matan dakeson daddy Dan sosai mata ke kawomishi hari,Amma ya na matukar taka tsan-tsan tunda yaga banso,Nikuma hakan kesani yimishi uzuri.
[5/24, 4:23 PM] Maman Dije: 66

A daidai wannan lokacinne wata tafiya ta tasoma daddy zuwa kasar Germany yaso kwarai tafiyar yaje dani Amma hajiya kaka tace bata yardaba garadai abarni gida tunda jikin nawa bawai warwarewa yayiba bazata yarda ajedani wata uwa duniyaba,saidai duk lokacinda yasami dama saiyazo yaga iyali,Kokuma yai hakuri harya dawo tunda wata uku ai kamar gobene indai da rayuwa.

Sam beso hakanba Dan sosai hankalinshi yatashi yatsara komai na tafiyar dani sabida yanda zaiji dadinshi Amma kuma gashi hajiya ta hana komai.

"Aunty daga gidan hajiya kaka mukefa ga daddy can ta kunnoshi.

Dan kaimishi mangari nai ina dariya kai Sadiq kabani DA gulma wallahi, Gayamin meya faru?

"Kedai bari kawai aunty akan maganar tafiyarshine Ashe wai dake ya shiryata Aiko yanzu tace bata yardaba,Kumama shima daddy ai da laifinshi yanzu Dan Allah yatafi dake har wata uku makarantarki fa,Sannan mukuma muyi yaya? Aigara data hana wlh.

Murmushi nayi,Wai kace yau akwai bakin rai wajan daddy saidafa na nunamishi yayi hakuri zuwa gaba Amma ya nuna ba hakaba sabida Allah yanda nake yanzu kusan kullun saina kwanta haka kawai injecan in kwanta babu wanda zai kuladani aikaga ankaini makasa.

Dariya yasaki kamin yakuma rufe bakinshi gudun kadda daddyn yajishi"Kinga yanzu kije kiji yaya ake ciki Dan DA alama saikinsha lallashi.

Allah ya shiryaka Sadiq kaima ka lalace wallahi,Zahra duk ta bataku,Jirani indawo inzo ka kankaremin farcena.

Rayuwa kenan Sadiq shine ya kasance k'awa agareni yanzu sabida tsabar shakuwar damukayi dashi sabida shi yanada hankali yasan damuwa da farimciki bakamar faruk DA Mimi ba.

""***""

Najima dayin Sallama amma naja na tsaya nakasa shiga sonakeyi na aroma kaina fuskar damuwa kaddama inshiga ya ganni wasai yaji babu dadi balle yanda nasan irin kwallafa ran dayayi akan tafiyar Dani din.

Banji takunshiba saidai kawai naji tattausan hannunshi cikin nawa yajani cikin Dakin"baby ya kikatsaya baki shigoba ko bakiji na amsa sallamar bane?
Naji daddy hakanan na tsaya.

Zama yai kan gadon kamin ya dorani saman cinyarshi ya maida habarshi akan wuyana tare da lumshe idanunshi yana Sauke numfashi.

Jinai tausayinshi ya kamani amma haka na daure ina sauraren saukar numfashinya,Yajima ahaka Sannan naji yafara yawo da hannuwanshi zuwa sassa daban daban najikina.
Jin yanda yake murzarmin kirji yasani furta"Daddy"

"Uhumm" shine abinda yace batare da yayi maganaba.

Tun yana murzata ahankali har tafiya tai nisa Amma ban nuna bansoba dannaga lallashin yake bukata,Da kanshi ya rufe kofar dakin Sannan yadawo gareni Dan yariga yagama tonoma kanshi,Ai ni wallahi rashin tafiyarnan dani gaba ta kaini nasan Zan huta hatta kiba sainayi kamin ya dawo.

Koda yaushe daddy yakanzominne kamar saban shiga ko bakonyi shiyasa har mamaki nakeyi wallahi idan yanzu muka kwanta anjima zaikara saiyayi wannan zalamar saidai na danganta hakan da yanayi na Dabi'arshi.
Duk wani Abu me sunan maganin Mata tuni na ajiyeshi gefe sabida cikin jikina gakuma bakar wahalar danakesha wajanshi aduk lokacinda ya bukaceni nagadai ina dalili ai bammayi shawara da zahra ba na ajesu dan dama kusan duk ita kebani tafini wayewa a wannan harkar.

Yamma lis yasami nutsuwar dayake bukata Dan KO la'asar nidashi mukayita cikin daki.

Bayan mun idar inata kokarin inkwanta inda nagama sallar,Saigashi ya tarairayoni jikinshi ya na murmushi"Babyna kingaji ko? Sannu Allah yaimiki albarka yabaki farinciki fiye da yanda kike farantamin.

"Ameen dadynmu nagode sosai.

Murmushi yakuma saki tare da shigardani cikin jikinshi,Harwani lumshe idanuna yakeyi, Wani irin shauki ke dawainiya dashi musamman idan ya tuno da wata irin nutsuwa dayake samu aduk lokacinda ya Tara dani, Shiyasa daya tuno zaiyi watanni har uku babuni saiyaji wani irin mummunan faduwar gaba ta sameshi.

Ajiyar zuciya yakuma saukewa kamin ya lallaba ya kwantar dani duk da cewa idanuna biyu lokacin shine yai tunanin ko barci yayi gabadani.
Ina kallo yana hada kayanshi anatse wanda zaiyi tafiyar dashi Sannan yamike ya fice falo inda yakejin hayaniyarsu.

***

Anatse yake tambayarsu duk bukatarsu yana rubutawa Dan kaddama ya manta,Sannan ya kalli Sadiq kai tashi muje kasuwar,Kukuma faruk kutsaya gida sabida auntynku na barci kadda gidan yai shiru dayawa.

Agogo na kalli bayan fitar daddyn naga kusan biyar saura gashi gobene tafiyar dadyn dandai bada wuri jirgin zai tashiba Dan sai bayan azaharma Wanda zaikaishi abujan zaitashi.
Adacan ya shirya tafiyar danine sukuma yaran su zauna wajan hajiya kaka shiyasa ko kayan amfanin Gida babu abinda yasiya,Yanzuko tunda tafiyar tafasu shiyasa yanufi kasuwa dansaimana kayan bukata.

Da sauri na mike inafadin banga ta zamaba dole inyimishi abun bukata kamin ma yadawo ya hanani.
[5/24, 4:23 PM] Maman Dije: 67

Faruk shine ya dinga kamamin aikin Dan haka nima daurewa nayi na yakicema kaina gajiya da kasalar danakeji na zagade aiki tunda nasan idan nayi lallai zaiji dadi.

Cikin kwanciyar hankali naimishi wani lafiyayyen cincin manya Wanda yaji kayan hadi dan sosai natsaya na gyarashi,Saida na nade Wanda zaiyi tafiyar dashi cikin takarda sannan na Dora dahuwar kaji kamar yadda nai niyya.
Ana sallar magriba ina tuyarsu,Wata irin jar suya naimusu me matukar kyau da tsari dan inaso inya gani yaji dadi kuma ya yaba.

Saida sukai sallar isha'isannan saigasu sunshigo kowa hannunshi niki niki DA kaya,Nanfa suka baje falo da alama sungama gajiya.

Duk sannu mukaimusu Sannan nakawo ruwa nabawa daddy dannasan ya na bukatarshi.

Ganin inata shige da fice daga falo zuwa kitchen yasashi tambayar"Me kikeyine haka kikakasa zama waje daya?

"Daddy nama Zan soya"

"OK to bari inshiga ciki inkin gama saiki sameni.

"Ah daddy to abinci fa?

"Share kawai Jidda yanzu cikina acushe yake inaga dai zuwa anjima zansha coffee.

***

Cikin iko na Allah lokacinda 11;00 na dare yayi munkammala komai nida Sadiq nagaji sosai da sosai,Amma haka na daure saida naga komai ya daidaita hatta jakar da zanzuba kayan ciki na tanaza sannan nawuce dakina Agurguje nai wanka tare da sallar isha'i lokacin hatta Sadiq din ya kwanta ,Sannan na wuce wajan daddy jikina Nata tashin k'amshi.

Shi kanshi tuni yai barci danhaka rabawa nai gefenshi tare dayin addua na kwanta.

Shafar da akemin ta tilastamin tashi daga daddadan barcin daya kwasheni dannagajine sosai da sosai.

"Cikin dan magagi na furta daddy please!!!

"Sorry baby na ni kadai na dameki ko?Kiyi hakuri zamuyi na bankwanane kinji?

"To sakarni na wanko bakina"

Hannuwanshi ya mikomin gabadaya ya na kallona cikin hasken wayarshi"Wai aikin me kikayi dazu ne harnagaji da jiranki nai barci?

Wata k'atuwar hamma na sauke Kamin nace"Daddy kabari muyi barci Wallahi nagaji mana kawai na gyara kuma nida Sadiq mukayi komai.

. Da gaske na bankwanan yakeso muyi Dan sosai ya murjeni son ranshi,Sannan ya kyaleni bayan yagama tabbatarmin da zaikuma tashina idan na huta.

Ko wanka bansami sukunin yiba sabida tsabar gajiya danayi.

A tunanina ko barcin kirki banyiba,Kawai naji yana lalubata,Yinai kamar zansakamishi kuka Dan sosai gabbaina ke ciwo"Ni Dan Allah ka kyaleni wallahi banso"

"Hakuri zakiyi Jidda danatafi fa shikenan saikuma nadawo shine kuma kike nema ki hanani kanki?

Tunda naga bawani lallashi ko ban baki zaijiba dole saina hakura naja bakina na tsuke ammafa zuciyata inajin babu dadi.

Tun kamin tafiya tai nisa nafaramishi kuka,Sabida yanda wajan yakemin wani ciwo Dan dama dazu sosai ya nukurkusheni gawani DA dare yanzuma ya kasa ya tsare zai kasheni.
"Wayyo daddy Zan mutu wlh saura kadan wayyo Allah Hajiya zai kasheni.

Duk irin Ihu da tirje tirjen danakeyi be hanashi abinda yakeyiba Dan sainaga kamar ma batani yakeba ko beji kokuma ya daina fahimtata,Gashi wannan karan yaki samin nutsuwa da sauki, Sosai nafita hayyacina.

Bazance ga iyakar lokacin daya daukaba Dan saida nadaina gane komai Sannan najishi ya kwanta gefena yana sauke numfashi.

Jin nakiyin shiru yasashi jawoni jikinshi shikenan yi hakuri bazan kumaba"
Banza nai dashi sosai nakejin zafi Akasana Dan gaskiya akwai matsala kilama yajimin ciwo.

"Zafi sosai daddy"

"Subhanillahi sannu Ina zuwa.

Ruwan zafi ya hadamin bayan ya gyara jikinshi,Ina daga kwancen Amma zuciyata tashi kawai takeyi ga wani irin hautsinawa da cikina keyi.

Yana dagoni nafara yunkurin amai Dan haka da saurinshi yaisama dani zuwa toilet din,

Saida nai aman duk wani Abu danaci cikin daren sannan nasami nutsuwa,Yayinda shikuma duk ya rude sabida yasan hadda wahalar danasha ta tilastamin wannan aman.

Ina kwance ina sauke numfashin wahala shikuma yana gefena zaune yama kasa kwanciyar saiwani jijjigani yakeyi yana matsamin jikina,Har saida yaga barci yai gabadani sannan shima ya kwanta.
[5/24, 4:23 PM] Maman Dije: 68

Alhamdulillah Lafiya lau mukai sallama da daddy,Sai bayan yatafine nafara ramuwar barci Dan sosai yabarni da ciwon jiki,Yaudai zahra babu bakin magana domin itama tunda ya usi yakawota Dan yima daddy din rakiya taketa bin kujera duk inda tasamu kwanciya takeyi da Alama itama irin lalurar data dameni takeyi.

Taso ta zauna gidanmu Amma ya usi ya matsa lallai su wuce tunda batajin dadin jikinta,Nidai da idanu nabisu dannima ta kaina nakeyi.

""""***""""

Bayan wata daya:  Kwance nake saman gadon daddy wata irin masifaffar kewarshi ke damuna abinda bantaba tunaniba balle inkawoma raina,Duk inda na juya kamshinya nake shakowa gashidai ya kwana biyu bashi cikin dakin dan hatta zanin gado na canza Amma k'amshin turarenshi na kewaye da dakin.

Kuma juyawa nayi tare da shafar dan Matashin cikina dake lahe cikin marata,Shi kanshi cikin yai kewar dadynshi kwana biyu beji an tabashiba.

Inajin wayata tana ring amma wata kasala ta hanani ko motsin kirki balle in dauko wayar, Saida aka kuma kira akaro na biyu sannan na dauka batare dana duba wake kirabama.

"Hello"

"Hey babyna kunyini Lafiya ya little babyna?

Wani siririn kukan shagwaba na sakarmishi,Wanda na tabbata saiya kassara kuzarin jikinshi.

"Subhanillahi sorry babyna waye ya tabamin ke haka? Uhum gayamin waye?

"Daddy nagaji Dan Allah kadawo wallahi kewarka ta isheni,Ko dadin barci banaji kullun bakanan!!!

Cikin wani irin farinciki ya kwashe takardun dake gabanshi tare da mikar da kafafunshi yandazaiji dadin sosai ,Dan wata irin kasala yaji ta saukarmishi lokaci guda ga uwa uba kuma shima kewar data addabeshi.

Ba k'aramin Dadi yajiba musamman dayaji wai Jidda na kewarshi ashedai hasashenya yazama gaskiya cewa matarshi tafara kaunarshi Ashe dai hakanne.

"Alhamdulillah ya furta cikin zuciyarshi kamin yace"Kinga kwantar da hankalinki kinji,Kinga yanzu har nayi wata daya da tafiya hadda kwanakima insha Allah kamar yaune zaki ganni gabanki na dawo Amma bansan injiki cikin damuwa ko kinaso inkasayin aikin daya kawoni?

"Uhum uhum" shine abinda na furta cikin narkewar murya.

"Ok to ki kwantar da hankalinki zandawo kinji? Ya cikinmu yafara girma kuwa?

Dan shafar cikin nayi kamin ince"Kadanne daddy.

Murmushi yasaki Wanda harsaida naji sautinshiKamin yace to Alhamdulillah aidama ahankali ahankali yake girma kinga lokacinda zandawo nasan ya girma sosai,Zantaho da kayan baby masu kyau insha Allah,Ashe itama zahra cikin ta samu?

Kuma marairaicewa nayi,Eh fa daddy Amma ita batayin amai saidai zazzabi Amma ni kullun sainayi.

"Ayya!! Sorry kema zaki daina kullun inayimiki addua gakuma lada da kikesamu ko? Kedai kita hhakuri har indawo saina dinga tayaki,Kinadai dansamu kici wani abun ko?

"Eh daddy inaci Amma ba sosaiba.

"To shikenan Ammadai bawata matsala ko?

A a akwai daddy Mimi ke fama da mura Amma naba Sadiq kudi yasiyo Mata maganin mura nan gidan babu maganin mura.

"Ok to hakan yayi Allah yaimiki albarka,Zankiraki kamin ku kwanta saimu gaisa da yaran.

Cikin shagwaba na furta Dan Allah daddy inkasami lokaci kadawo inganka wallahi nagaji DA rashinka komai yadaina min dadi.

Wani murmushin jin dadi yasaki kamin ya shafi sajenshi"Karki damu autar mata insha Allah,Nasan nafiki jin kewarnan musamman Idan na tuno da daddadan kamshinki da laushin fatar jikinki sai inji  Ina neman zaucewa balle idan na tuno da lafiyayyar ni'imar jikinki baby Allah nayi kewarki irin sosai dinnan,Amma gayamin idan nadawo mezaki tarbeni dashi?

"Allah daddy duk abinda kakeso shizan baka indai zaka dawo din.

"Ok to shikenan kin yarda babu korafi kuma babu kuka ko?

Cusa kaina nayi cikin filo kamin nace kai daddy!!!

"Eh mana kadda danadawo adinga kuka aka kiran wayyo hajiya daddy zai kasheni.

Kashe wayar nayi Ina dariya dan sosai yabani kunya ashedama yanajin duk ihun danakemishi Amma saiyaiwani biris dani yakoma kamar kurma.

""""

Ahaka mukacigaba da rayuwa cikin jin Dadi da farinciki hhankalina kwance haka na 'yan uwana sabida bantaba zuwa nace gawata matsalaba,Duk da sunaganin kamar basu kyautaminba na auramin babban mutun amatsayina na yarinya me k'ananun shekaru,Saigashi hakan ya kasance alkhairi ga rayuwata,Kusan yanzu Sadiq shine ke komai na gidan sabida yanayin jikina Amma kullun nikeyin girki,Sam yaran basu dawata matsala.

Shiyasa nakesonsu kamar kamar me,Kuma suma haka suke kaunata,Dan idan har sukaganni kwance to suma kamar marasa lafiyar haka suke komawa inko inayin amai ai har rige rigen zuwa yimin sannu sukeyi.

Alhamdulillahi bangaren makaranta banda matsala dan yanzu kullun inazuwa koda inajin ciwon ina kokarin daurewa balle hajiyata kullun k'ara wayarmin dakai takeyi akan dukkan abinda yashafi harkar cikin hakama hajiya kaka duk asabar da lahadi nan takeyini tare damu.

***

Zaune muke Muna hira sai kwasar dariya mukeyi,yayinda faruk da Mimi ke tausamin kafafuna dasuka dameni da ciwo yau tunda mukadawo makaranta.

"Kunga gobe tunda babu islamiyya dawuri zamudawo makaranta to mu wuce gidan zahra Kawai muganota kunga yauma bataje makarantaba.

Faruk ne yaimin sigina yana kallon Mimi Dan daddy yahanamu fita kwata-kwata to shine damunfita itake gayamishi.

Riko kunnuwanta nayi tare da zaromata manyan idanuna"Kinsan Allah Mimi idan kikagayama daddy munfita sainasa yaya Sadiq ya mikama karnuka ke kuma bazamu kuma fitadakeba saidai ki zauna gida keda megadi.

Bakinta ta turogaba kamintace nabari aunty bazan kumaba kumama AI daddynne ke tambayata Ina mukaje

Harararta nayi kamin ince nadaigayamiki Allah kuwa.
[5/24, 4:23 PM] Maman Dije: 69

Tun asuba yau ban komaba sabida samakaina zuwa gidan zahra danayi, Saida mukagama

aikin komai sannan na hadamana tea kawai mukasha muka fice,Bantsaya yin girkin ranaba sabida nasan bazamu dawo gidan da wuriba.

Aiko yauba batazo makarantarba saidai waya da mukayi tace da sauki Sosai.

Wani bata fuska isiya Direba yayi lokacinda nace ga inda zai kaimu.
Banza nai dashi Dan karma yaga fuskar tambayata nasandai daddyne yagama yimishi kashedi akan kaimu wani waje.
"Isiya ko muhau napep ne?

Sosa kanshi yayi A a hajiya muje Ammadai bazaku jimaba ko?

Sadiq ne yadan harareshi,Kamin yace Sannu daddy"

Duk dariya mukasaki sabida yanda Sadiq din yai maganar,To dama kowa yagaji da zaman gidan,Balle kuma su maza musamman shi Sadiq din dayafara girma ko kwallo dadyn ya hanashi fita kuma ga yara nayi irinta cikin unguwa haka.

""**""

Kai gaskiya ciki manyane,Duk karadinnan na zahra babu shi tai laushi sosai gashi sai aikin Tara miyau takeyi abaki.

Dariya nasaki sosai hadda kwanciya ganin yanda taiwani dai-dai Saman kujera daga ita sai bes idanu duk sunfada.

"Hahhha wayyo dadi kasheni,Zahra kintuna iskancin da kikrmin akan wai Dan naga daddy na lallashina shiyasa nakekuma lauyewa to yau gakinan ba baka sai kunne.

Hararata tayi ta mike taje ta zubar da miyan bakinta,Saigata dawani danyen lemon tsami waishi take lasa, kutt Ammadai cikinnan ya kwareki da yawa wlh.
Zama tai tare da yamutsa fuska,"Dan Allah kidaina dariya aunty wallahi gabadaya banjin dadin rayuwata yanzu nifa cikinma harnaji bansanshi wlh.

Murmushi nayi kamin ince Wallahi zahra garake kinacin abinda kikeso kuma ya zauna tunda bakiyin amai Amma nikumafa? Ko ruwa nasha wani lokacin sainayi amanshi,Kuma rabon da inci wani abinci mesunan abinci harna manta saidai yame yame suma bakowanne ke zamaba,Kinga ko ai gara ke.

"Eh hakane gaskiya gara ni inaga so biyu kawai natabayin amai wlh Amma yanzu haka jinake duk nagaji dashi, gaskiya Allah ya sakama iyayenmu da mafificin Alkhairi.

"Ameen kedai bari kawai wani lokacin bansanin ina hawaye sainaji zubar ruwa sosai cikinnan ke gwalani wai yanzuma kinsan abunda ke damuna kuwa?

"A a inafa zansani saikin gayamin.

"Wallahi zahra wata irin kewar daddy ke damuna, Sosai nakejin damuwa aduk lokacinda natuna yaimin nisan da zaijima bai dawoba,Gashi indare yayi ko barcin kirki ban iyawa sosai sabida tunaninshi.

"Hahhhhha wayyo dadin duniya,Allah dai ya biya daddynmu,Alhamdulillah,wallahi naji dadi sosai ashedai daddy beshiga zuciyarki da wasaba!!! To hakan yayi Amma yakamata ki gayamishi danyai kokarin shigowa tunkamin kewar ta tabamana baby tunda kince baki barci sosai,Ah Lallai Abu yayi kyau.

Jingina nayi da kujera tare da lumshe idanuna,Tunanin tattausan Lib's dinshi ya fadomin da irin zazzafan kiss dinshi, jinai gabadaya tsigar jikina tatashi,Bude idanuna nayi na saukesu akan zahra dake aikin kallona tana sakin murmushi.

Dan tsaki naja tare da kauda kaina ga barin kallonta danna lura shakiyanci cikin jininta yake, dangashi bata da Lafiya Amma ta na nema naimini hakan.

''''''''''''

Akace kwanci tashi asarar merai,To lallai kam dangashi kamar yaune daddy yai shirin tafiya saigashi yanzu da watanni uku hadda sati dayama.
Zuwa wannan lokacin gabadaya nafita hayyacina kumafa karkuyi zaton laulayin ya maidani haka A'a ko kadan kawai tsabar kewar mijina ke wahal Dani kullun da tunaninshi nake kwanciya kuma dashi zantashi duk da cewa koda yaushe muna waya dashi danwani lokacinma idan yakira da dare tofa sainayi barci yake kashe wayarshi,Duk kuma aikin lallashina yakeyi Amma duk da haka bangane komai nidai kawai bukatarshi nakeyi kusa dani.
Gashi sunkuma bashi sati biyu akan wata ukun da yayi.
Ranar dayagayamin cewa sunk'aramishi sati biyu saida naimishi wani k'aramin hauka sabida tashin hankali da damuwa,Dan nasa rai sosai DA zuwanshi,Ranar nan Hajiyata da Hajiya kaka suka yini suna lallashina Amma haka na yini kuka.

Iyakar tashin hankali ya shigeshi Sosai yaji aikinma ya ficemishi arai sabida halin danashiga.

Bayan kwana hudu; Kwance nake Ina barci kasancewar yau asabar tun safe nake kwance sabida kwalemar da mukayi jiya saida mukaima gidan tas Sannan muka kwanta.

"Aunty,"Aunty daddy na kiran wayarki.
Yamutse fuska nayi kamin ince"Kai Sadiq nacefa kabar tashina idan ina barci ko kanaso kaina ya isheni da ciwone?

"A 'a aunty yi hakuri naga daddyne ke kiran ko yanada muhimmanci kiran shiyasa na tasheki,Kumama ai yakamata kitashi hakanan kici abinci.

Amsar wayar nayi Ina tambayar"Kai Ina Mimi karfa kabari tafita waje mubani kaga jiya hakatai shi megadi yanacan yana gyangyadi zata fice ta barshi.

"Hello daddy,

Ajiyar zuciya ya sauke kamin yace"Uhum amaryar daddy ya kuke ya jikinki?

"Alhamdulillah daddy komai lafiya.

"Masha Allah Amma yanaji muryarki haka babu matsala ko?

Tashinai daga falon na nufi dakinshi,Saida na kwanta tare da rungume filo Cikin jikina"Daddy Dan Allah kadawo hakanan wallahi nagaji nakusa komawa wajan hajiya tunda bazaka dawoba.

"Ah subhanillahi kadda muyi haka dake Dan Allah ki rufamin asiri zandawo ko zuwa jibi ne hakan yaimiki?

Cikin zumudi da murna nace DA gaske daddy?

"Insha Allah babyna indai hakan yaimiki ba matsala zanyi duk yanda zanyi danganin nazo gareki,Amma yaya kikejin cikinmu yana motsi Lafiya lau ko?

Hannuna nakai na shafashi kamin nace yanayi daddy komai Lafiya lau,Amma dai DA wuri zaka dawo ko?

Wani k'ayataccen murmushi yasaki Kamin yace kadda kidamu duk yanda kikeso autar mata.

Cikin farinciki yaudai mukai sallama kamin infice falo ina murmushi,Hannu na mikama Sadiq muka kashe kamin ince yaro daddy jibi ya na nan tafe.

Tsalle yai ya dire saman kujera Ammadai naji dadi wallahi haba aigara yadawo Abu wata da watanni.

"To yanzu Sadiq ta Ina zamu Fara gyaran gidannan?

Idanunshi kalar na daddy ya fiddo waje kamin yace Kai Aunty kibari Dan Allah yanzu kuma me wannan gidan yayi? Inacewa Allah yabani Mata me tsafta kamarke Amma gaskiya yanzu na canza gara wadda batakaikiba yo aunty ai taki tayi yawa wallahi,Dannasan wataran amatsayina na megida haddani zantaya aikin.

Dariya nasaki me sauti"Kai Sadiq yanzu sabida Allah sharri zakamin ?

"Bawani sharri wallahi ai idanma daddy yaji kina wannan aikin DA cikinnan wallahi saiyayi magana sabida Allah jiya inane bamu toneba cikin gidannan saikace injina haka kika maidamu kuma yau kice ya za ai? Tab ai Allah sai ingudu gidan Hajiya kaka inyi zamana.

Murmushi nayi to shikenan naji yanzu saimu canza zannuwan gado da labulaye Ammafa sai gobe danni kaina har yanzu jikina ciwo yakemin.

"Ahaf aidama nasan dole kiji ciwon jiki yanzu Allah ya kaimu goben lafiya saimu canza abinda kikace din,Amma me zamu dafa da darene yau?

"Kagane ko Sadiq kawai kabari idan kafita magriba ka siyomana tsire can tsallake,Wallahi kasalar girkin nakeji.

"To shikenan Allah yakaimu aunty,Allah ya rabaki da cikinnan Lafiya muma muhuta da ganin rashin lafiyarki.

Ranar litinin babu yanda Sadiq beyiba muje makaranta Amma nakiya nafison dai muyi komai anatse balle inaso inyima daddy abinci nagani na fada,To idan naje makaranta karfe nawa zandawo kuma harmuyi abinda yakamata.

Lokacinda Sallar azahar tayi ai tuni komai ya daidaita hatta wanka munyi jiran shigowarshi kawai mukeyi,Musamman ni danakejin kamar inyi tsuntsuwa inganni cikin faffadan kirjinshi.

Mimi ce ta rabo jikina"aunty zai dawo kuwa?

"Zaidawo mana Mimi bakiji tun dazu yace sun saukaba nasan sunkusa karasowa

yanzu,Zaikuma dawo Lafiya insha Allah.

Hon..din motar daddy yasamu mikewa gabadaya muna rige rigen ficewa dan ban yarda su rigani zuwa gareshiba kowa tashi ta fishsheshi.

Fitarmu harabar gidan da gudu yasa daddyn Saurin fitowa daga motar bakinshi hangame ya na niyyar dora hannu aka,Be Bari mun karasa gareshiba ya iso da sauri ya hademu gabadaya ya rungume yana dariya.
Jinai harwata hajijiyar nishadi ke neman kayar dani lokacinda najini cikin jikinshi.

Cikin kunnena ya radamin"Anya Jidda kinada hankali kuwa da wannan abun ajikinki kike gudu salan kijamin asara ko?

Duk ficewa mukai daga jikinshi muna dariya kowa fuska awashe, Shikuma saiya dauki Mimi akafadarshi yakama hannun faruk zuwa cikin gida.

Sadiq shine ya shige gaba danhaka shine zaifara aiwatar da shirinmu na farko dan tarar daddyn.

WELCOME HOME  DADDY.
SHIne Abu nafarko dayafaramishi Sannu da zuwa Dan jikin kofar shiga falo muka likashi.

Juyowa yai tare da kashemin ido daya ya na murmushi.

Wasu kankanan takardu suka fara zubowa masu kamshin gaske lokacinda ya zura kafarshi cikin falon gawani mayen kamshi dakekuma gauraye ko Ina na falon Dan sosai kamshin keda daukar hankali.

Lumshe idanunshi yayi gabadaya yanajin wani irin matsanancin farinciki dakekuma baibaye zuciyarshi,Alhamdulillah ya Allah,Allah na godemaka da dukkan Alkhairinka gareni Allah Kaine abun godiya.

Kuma rungumemu ya dingayi daya bayan daya tare DA mannama kowa Sumba agoshi.

Kan kafet ya zauna tare da mike kafafunshi yana kallon inda tsafta take,Saika rantse da Allah sabon gidane ba a kaiga tarewaba tsabar yanda ko Ina yake tsaf ya na sheki.
Duk gaidashi mukayi ya amsa yanata murmushi yayinda yaketamin wani zazzafan kallo me matukar ratsa jiki.

Be matsa konan da canba Sai bayan la'asar lokacin yaci ya koshi kuma munsha hira.
Sannan yace na hadamishi ruwan wanka Idan Zan iya dannaga kinyi nauyi ashe.

Dan murmushi nayi kamin na mike Ahankali,Haka ya bini DA kallo cannaji ya na tambayarsu "auntynku nacin abinci kuwa yanzu.

Nagama hada ruwan Ina niyyar fitowa Saigashi yashigo dagashi sai gajeran wando fa



"Sannunki dai autar mata Ashe haka abinmu ya girma Sannu bedai baki wahala ko?

Dan lumshe idanuna nayi inakuma shigewa jikinshi,Jin wani irin waiwayi dayakemin.
Ganin nakasa magana yasashi Shigar Dani jikinshi sosai"Naga alamadai babynnan namu daddy yake buk'ata bari infara Sallamarshi tukunna.

Idona nadan fiddo inason inyi magana,Amma ina tuni ya cafki bakina dannaga shima amatukar bukace yake yandanaga jikinshi nata rawa.

Saida komai yai nisa Sannan ya daukeni zuwa gadonshi wankan da beyuwuba kenan.

"Uhum daddyy, "Karki damu jiddana Ahankali zanyi komai ainasan ankwana biyu ba'a haduba.

Yes gaskiyane munyi kewar juna irin wacce tafi karfin abada labari.

Ba k'aramin wajagalgalina yayiba,Ammadai na daure banyi kukanba,Ammafa na kusa Dan Sosai na galabaita.

"Hummm wayyo jiddana nagode Allah dayabani ke nasan kina dayadaga cikin matan Aljanna,Allah ya jikan mahaifanki hakika kin sun iya haihuwa.

Kamar inyi dariya  Amma na fuske dan jin yanda yaketa sambatu,Karma yaran su jiyomu duk da akwai tazara sosai tsakaninmu.
Hannuna nasa na rufemishi baki,Wanda ya tilastashi yin shiru.

Irin nacewar da yayi yasa jikina yaiwani mugun laushi sabida jigata ga tashin zuciya.

Rungumeni yayi muna sauke numfashi,Ahankali ya matseni cikin jikinshi tare da harde kafafunmu cikin na juna ya na kallon fuskat,Wadda tai zufa gakuma lemar hawaye cikin idanuna.
Wani k'ayataccen murmushi yasaki,Zuciyarshi ta wadatu da farinciki.

"Idanuna arufe na furta daddy"

Kasancewar idanunshi nakan fuskata yasa ya fahimci sunanshi nakira Dan sosai muryata tai laushi da yawa.
"Uhumm Autar Mata inajinki.

"Daddy cikina"

Da sauri yakai hannunshi saman cikin yanafadin"Sorry ya takure waje daya ko? Sannu hadda rashin Sabo zai daina kinji.
Ahankali yaita shafamin cikin zuwa wani lokaci ya warware daga takurewar da yayi.

""""***""""

Sai daf DA magriba na ta shi kuma ko wanka betasheni nayiba,Na juya naganni nakadai saman gadon danhaka Ahankali natashi zuwa bayi saida na tsaftace jikina Sannan nasaka doguwar riga Mara nauyi na nufi falo can nakejin hayaniyarsu.

Duk maido idanunsu sukai kaina lokacinda na isa falon,Sannun da suketa jeramin yasani kallon daddy tare da tambayarshi DA ido,Saikawai yayi murmushi tare da kannemin ido daya.

Zamanai tare da kallon faruk,Da sauri yaron yawuce kitchen,Saigashi da lemon fanta Dan yanzu kusan shine abincina, Ajewa yai gabana ya na fadin gashi aunty.

Ansa nai nacigaba dasha Ina lumshe ido, Yayinda daddy yabini DA kallon sha'awa gaskiya tsarin gidanshi na yanzu ya na matukar birgeshi,Komai saimun tsarashi sabida gashi yanzu banyi maganaba Amma ankawomin abinsha yasan cewa kila shine aikin faruk din aduk lokacinda natashi barci.

"Amma Jidda babu sanyi wannan fantar?

Dan turo bakina gaba nayi Kamin ince akwai Amma kadanne daddy.

"To naji ku shirya muwuce mu gaido hajiya banshiga wajantaba tunda na huta,Kuma Dan Allah Kadda ace za'ai wani girkin Ahuta hakanan.

Nashiga d'aki da niyyar canza kaya saigashi ya shigo" Jidda inzo in tayaki ko?

Dan murmushi nayi Ina kallonshi"Daddy kaya kawai zansaka ai.
Matsowa yayi tare da sagalo hannunshi akirjina yanadan matsawa ahankali tare da lumshe idanunshi.

Kuma maida bayana nayi cikin jikinshi,Aiko naji kamar yana cikin buk'ata dannaji alama, Kokarin kwace jikina nayi,Amma ya kuma damkeni cikin jikinshi har lokacin bebar latsar kirjinaba.

Ina jinshi har saida ya gaji dan kanshi sannan ya juyodani muna fuskantar juna,"Inasonki sosai jiddana Allah yarabaki da babynnan Lafiya .

Zagaye hannuwana nayi bayanshi,Inajin wani mashahurin dadi, Nima inasonka dadynmu.

Matseni yai jikinshi yana dariya"Nagode autar mata Allah yaimiki Albarka muje in shiryaki.

Kusan shirin na daddy ma duk tabe-tabe yafi yawa musamman kirjina da sukai wata cika yanzu gwanin ban sha'awa.

""***"""

Bayan dawowarmu daga gidan hajiyakaka sai mukawuce gidan hajiyata dama nakwana biyu banjeba,Dan haka da guduna na rungumeta Ina murna.
Runtse idanunshi yayi harsaida nashige jikin hajiyar sannan ya bude yana sauke ajiyar zuciya"Kai Jidda tacika wauta da cikin nan gaskiya".

Muna nan gidan harwajan Tara nadare Sannan yace mutashi mu wuce dama dagani sai Mimi faruk da Sadiq sun makale gidan hajiya kaka.

Ahankali yake tukin motar hannunshi daya na cikin nawa yana murzawa,Hira yakemin kasa-kasa itakuma Mimi na baya tanafama da cincin din da hajiya tabata.

"Amarya me zamu tsaya mu siya ahanya.

Dan murmushi nayi kamin ince daddy babu komai banajin yunwa ai Saidai ko Kai,Bakaga naci tuwo wajan hajiya ba?

"Eh naga kinci tuwo kuma naga kinyi amai to kinga akwai yunwa kenan, idan bakicin Abinci jikinki bazaiyi kwarin DA zaki iya daukataba ayanzu gakuma new baby Dan haka gayamin me kikeso sai in samamiki ko?

Kwantar da kaina  jikin kujera nayi tare da lumshe idanuna,Wani zullumine ya fadomin na tunanin suburbudar da zaimin da darennan gashi har yanzu jikina inajinshi sai ahankali.

[6/1, 1:14 PM] Maman Dije: 71

Ganin nayi shiru ban tankaba yasashi tsayar da motar gefen hanya ya zubamin manyan idanunshi yana kallona.
"Jidda menene?

"Uhum daddy nagaji wallahi jikina ciwo yakeyi"

"Ayya sorry kiyi hakuri bari mu k'arasa gida saina tausamiki jikinki inaga hadda wahalar da jikinki yayine yau.

Gasassar kaza kawai ya siya sai fanta me sanyi tunda ya lura ita nakeso.

Kamar yanda ya fada kuwa, DA kanshi yaimin wanka Sannan yaimin shafa,kuma ya kwantar dani yana gayamin kalamai masu dadi DA kwantar da hankali,wannan halin na daddy kekuma samin kaunarshi cikin  zuciyata tabbas kyautatawa itace jigon zaman aure,Domin duk gidan da babu kyautatawa hakika akwai nakasu cikin wannan zaman auren, Nagodema Allah dayabani daddy amatsayin miji agareni tabbas Allah ne ya dubi maraicina.

Saida ya tabbatar DA  barcina yai nisa Sannan yatashi shima yafara shirin kwanciyar danko wanka beyiba alokacin.

**""""**

DA Asuba,Tunda yatasheni Sallar asuba ban koma na kwantaba duk yadda yaso ya kwantar dani kuwa,Saida na kammala komai sannan nakoma wajenshi lokacin karfe shidda da rabi.
Rungumoni jikinshi yayi tare da sumbatar hannuwana"Yakamata ki rage aiki jidda kina wahalar da jikinki da yawa fa!!!

Cikin shagwaba nace daddy kabarni na dingayi bansan zaman kuma kaga yau babu masu tayani Amma Zan kiyaye zuwa gaba.

"Hakan yayi Allah yaimiki albarka,Yanzu ya zakiyi dani kamar hakurina ya kare fa,Ya idasa maganar yana kashemin ido daya.

Murmushi nasaki Ina gyara zamana cikin jikinshi"Kai daddy jiyafa kayi!!

Hannunshi yasaka cikin rigata"Tab kina wasa yarinya jiyama da dare dannaga baki iyawane,Kuma ga cikinnan danaga kamar yana takuraki shiyasa na hakura Amma wallahi banki in dawwama cikin ni'imarki ba.

Kauda kaina nayi Ina murmishi kai daddy ko.

Ganin da nai da gaske bukace yake yasani biyemishi tare dabashi cikakken hadin kai,Dan ya sami nutsuwar data dace,Kamin garin Allah ya idasa wayewa.

Aiko nasha wuya dan DA zazzabi natashi Dan barcin danakoma,Kuma koda garin Allah ya waye ya hanani zuwa makaranta saidai yakai Mimi to dama nagaji ko gardama banyimishiba kuwa.

""""***""""

Hausawa sukance tafiya sannu-Sannu kwana nesa,Hakance ta kasance kullun cinye kwanakinmu mukeyi batare da mun fargaba,Kamar wasa saigani da ciki wai harya shiga na Tara.
Alokacin dakyar nake zama hakama tashi Allah ya temakeni lokacin munyi jarabawar shiga ajin karshe,Zaune kawai nake kusan nazama abun tausai Dan cikin yagirma duk DA ya kasance cikin fari ne.
Alhamdulillahi Allah shine abun godiya haka wannan batu yake,Bani da wata matsala Zan iya cewa kowa sona yakeyi idanma akwai Wanda besona to lallai be bayyanaba,Yaran mijina kaunata suke kamar su cinye haka mahaifiyarshi,Musamman da cikina ya tsufa kullun tanakan hanya zuwa gareni dubani Sannan takanzomin da 'yan jike jikensu na mutanen dasuka kwana

biyu duk DA  cewa daddy dayagani yake zubarwa wai basu da wani amfani ajikina balle babyn, Kundaisan halin likitoci.

Cikin zahra itama yanzu wata biyar duk rawar kannan babu ita yanzu Dan anfara girma da hankali laulayi ya ladaftar da ita.

***

Kwance nake,Kaina bisa cinyar daddy Aiki yakeyi Amma hakan behanashi rungumataba lokaci zuwa lokaci yakan sumbaci gashin kaina Wanda yake atsefe Ammadai yasha gyara.
Tun inajinshi har barci yai awongaba dani batare danasaniba.

Cikin barcin nakejin kamar Ana tsikararmin Mara danhaka ahankali na bude idanuna tare da zubasu akan fuskar daddy domin shima ni yake kallo.
Yamutsa fuskata nayi Ina dafe cikina danakejinshi wani iri yau.

"Lafiya jidda?

"Banjin dadin cikinnan daddy yanzukuma marata nakeji tana tsinkulina.

Manyan idanunshi ya fiddo kamin yafara tattare takardun jikinshi,AAhankali ya tasheni zaune,Sannu kinji zomuje kiyo tattaki ko cikin haraba ne jikinki zai saki kinji?

Ya na rike da hannuna muke zagaye gidan,Hira yakemin Amma Sam komawa nayi bana fahimtarshi daga karshema sai kafafun suka ma kale, dole ya dagoni nida cikin zuwa cikin Dakinshi.

Wani irin ruwane ya biyo k'afafuna lokacinda ya direni cikin Dakina,Atsorace na kalleshi Dan tunanina ko fitsarine ya kuccemin.

Saidai tuni naga hankalinshi yatashi yafara gyare gyare, Ahankali ya zaunar dani Sannan ya gyara waje daya,Ya kamani ya maidani can.
Kallon Karin bayani naimishi danhaka saiya furta "Karki damu Jidda kiyi addua haihuwa zakiyi da izinin Allah yanzu ki daure kinji!!

Alokacin wani irin miyau na hadiye Dan gaskiya wani irin tsorone naji yatasomin gaba daya.

Dakyar nabari yasamin hannu DA sunan wai dubawa zaiyi yagani.

Aiko hadda safarshi ya budeni ya zuramin Hannu aiko kamar Ance ya zaro hannunshi wani

irin azababben ciwo yabiyo baya, kamin wani lokaci nafara murkusu da zufa.
[6/1, 1:14 PM] Maman Dije: 72

Har ya fara tunanin kaini asbt domin atrmakamishi ganin yanda nakudar tai tsawo,Tausayina yakeji kamar kamar me.

"Wayyo daddy nagaji Zan mutu.

Wani danasanin rashin yimin aikine ya tasomishi yasan DA aikin akaimin da yanzu bantsaya shan wannan azabar ba,To kuma yaduba Lafiya lau Zan iya haihuwa da kaina, Kawaidai tazo da jinkiri ne.
. "Hannuna ya rike yana shafar kaina kiyi hakuri Jidda zaki iya haihuwa da kanki kuma lafiya, Dan haka ki daure kinji.

Nidai inaga babu kalar abunda banyiba ranar,Dan saiwajan daf da magriba Sannan Allah ya temaka na haihu, Yarona namiji rusheshe dashi.

Hamdala yaja tare DA rungume yaron ajikinshi duk da irin dattin dake jikin yaron.

Lumshe idanuna nayi inajin wani irin dadi da iska,Kai haihuwa ikon Allah,Dafarko nai tunanin mutuwa zanyi kawai sabida azaba Ashe babyne zaifito duniya yau.

Agaskiya yakamata mukara kaimi wajan kyautatama iyayenmu misamman Mata wallahi wallahi ko babu laulayi babu sauran wahalhalu nakuda kawai ta isa tasa muyima iyayenmu biyayya,Hakika duk Wanda kedasu araye to lallai ya dage wajan kyautatamusu inko babusu sun rasu to ya nace wajan nema musu gafara.

Alokacinda yake kokawar gyara babyn nikuma alokacin kuka nakeyi, Inama su Ummana na raye in rungumeta in sumbaci ko Ina na jikinta,Inama Zan ganta in meni gafararta koda akwai abinda nataba Mata Wanda bansaniba,Duk da cewa sun rasune alokacinda ni bani da wayau.

Kuka nakeyi Ina jaddada nemamusu gafara wajan Allah.

"Da saurinshi ya ajiye yaron ya karaso gareni kiyi hakuri,Jidda addua yakamata kimusu bawai kukaba,Kasancewar yanajin Sambatun danakeyi.

Sai bayan Sallar isha'I Sannan yafara fadin ai na haihu.
Dan dama ita haihuwa haka take dakace gashican za ahaihun gara kai hakuri kace an haihu.

Acikin daren su Sadiq suka dawo Hajiya kaka da hajiyata kuwa kamar hadin baki Dan kusan tare suka shigo.

Nidai barcin gajiyane yaigaba dani vayan nagamashan tea duk hayaniyarsu bata Hanani barciba dannagaji yanda yakamata.

Alhamdulillah koda garin Allah yawaye ai jinai kamar sauyani akai sabida babu cikin jikina,Gakuma yaro kato dashi tubarkalla agaba wainice na haifeshi,Yo mamakin yanda yafito jikinama nakeyi wlh.
Hajiya taimin wanka kuma ta wanke baby,Yayinda Hajiya kaka taimin tuwo dakuma farfesun kaji Wanda yaji daddawa da kayan yaji.

Tun safennan saiga zahra da yaya usi na,Baki har kunne har rasa gane wanne yafi farinciki nayi.

***

Bayan watanni biyu,Zaune nake akan kujera Haidar nashan nono Saiga daddy yai Sallama.
Amsawa nai Ina murmushi"Sannu da zuwa daddy ina yini"

"Lafiya lau Jidda ya haidar?

"Lafiya lau,Tashi nai na mikamishi shi Sannan na wuce kawomai abun motsa baki.

"Uhum jidda ina hajiyar ne da Mimi fa?

"Aiko sunyi gidan zahra yau tatashi bata da lafiya.

"OK" Shine abinda ya furta tare da zubama yaron idanu danshima shiyake kallo,Tasbihi yakeyima Allah cikin zuciyarshi,Yaron kamar na larabawa duk yafi su Mimi kyau sabida shi farine tas ga dogon Hanci irinna uwa.
"Amma jidda har yanzu bakiyi tunanin komawa gidaba ko? Yanzu kindainajin tausayina wajan watanki biyu yanzu DA haihuwa inagama hadda kwanaki amma kinyi shiru abinki ga yaran ma sun gudu gidan Hajiya tunda sukaga bakinan itama Mimi ta likenan ya kukeso inyi?

Duk sainaji yabani tausayi Dan Idan idanuna ma ba karya sukeba sainaga kamar ma yadan fada.

"Daddy bawai banjin tausayinka bane wallahi inaji Ammadai inajin kunya ne tunda kaga su Hajiya basuyi maganaba aikaga bazance komaiba indai ba kaine zakai maganaba,Kuma gaskiya wannan yaron yacika rigima kadda in rasa yanda zanyidashi idan yafara kuka.

"Haba jidda yazakice haka gida cike DA yayunshi duk zamu tayaki insha Allah kuma bari injira Hajiya tadawo sainaimata magana Amma gaskiya hakuri na yakai karshe.
Cigaba da yima haidar wasa yayi yayinda yaron yaketa balle baki danyafara dariya.

"Tashi mushiga ciki mudan gaisa jidda!!!

Idanuna na fiddo waje"Kai daddy gaskiya a a kodawane lokaci Hajiya zatashigo kaga zamuji kunya taga munfito daga cikin d'aki tare,Ka k'ara hakuri dai har suyi tunanin komawar tawa.

Dan hararata yayi kamin yace"Lallai yarinya naki wasa,Amma gaskiya bazan iya ko kuma sati batare da kun komaba nayi kewar girkinki nai kewarka k'amshinki Sannan nai kewar ni'imarki Jidda wallahi nai kewar komai naki daurewa kawai nakeyi Amma idan basubani keba lallai nakusa dawowa gidannan da zama nima.

Dariya nasaki raina fes inajin wani madaukakin farinciki,Dan sosai nakejin dadi aduk lokacinda daddy ke kodani irin haka.

Muna nan zaune munata hira saigasu sundawo,DA gudu Mimi ta hayeshi tanayima yaron wasa,Yayinda shikuma sukacigaba da gaisawa.

"Am Hajiya Dama nazone intafi da Jidda zamukoma gida, Tunda naga takwana biyu DA ga ma wankan.

"Eh hakane kam habibu aima kayi hakuri,Amma Dan Allah kaimin hakuri ingayama iyayenta tukunnan daganan  zuwa jibi inshaAllah saimu maidomaka da matarka saikumafatan Allah yaraya abunda akasamu,Cewar Hajiya .

Wani murmushin farinciki yasaki Kamin yaimata godiya nikuma ya kalleni ya kannemin ido daya.

Mumushi Kawai nasaki Ina mamakin daddy wani lokacin sai yai Abu kamar yaro wallahi.

Hira suka dasa da hajiyar kuma har lokacin yaron na hannunshi,Mimi ma na like jikinshi tanayima haidar din wasa.

Sai dare sosai Sannan yaimana Sallama zai wuce.
Hajiyace ta kalleni ki rakashi mana jidda.

Adan kunyace nabi bayanta bayan na ajemata haidar din,Be juyo ya kalleniba saida yashiga cikin mota ya zauna,Sannan ya budemin bangaren ya na kallon cikin idanuna musamman da hasken nefa ya gauraye harabar gidan.

Dan turo bakina gaba nayi kamin in shiga,Ko kaiga zama banyiba ya rungumeni jikinshi tare da lalubar bakina, wani irin zazzafan kiss yakemin kamar zai cinyeni kamin wani lokaci ya ruda kanshi ya rudani tuni jikina yafara kyarma kamar yadda nashi ke tsuma,Muryarshi taiwani irin laushi ya furta"pls Jidda ko kadanne Dan Allah wallahi nagaji"

"Kayi hakuri daddy insha Allah jibine kawai kaga nan kodawane lokaci ya Usman zai Iya shigowa tunda bezoyaimana saida safeba,Nasan bazaka Sami nutsuwar DA kake bukataba kayi hakuri.

Matseni yayi jikinshi ya na sauke numfashi sosai yakejin wata irin masifaffar kewa, Bekuma tabbatar DA cewa Jiddan na kokari wajan biyan bukatarshiba Sai yanzu data kwana biyu basu tare duk dare dakyar yake runtsawa.

Anan mukai sallama yawuce nikuma nakoma cikin Gida tausayinshi duk yacika dabaibayeni.

Washegari;Hajiya da kanta ta rakani gidan me kitso da kunshi, Sai wajan azahar muka dawo abinci kawai mukaci ta hadani da matar baba habu ta rakani zuwa gidan gyaran jiki.

Aranar dai gyare-gyare naitayi haka kayammu tuni an ga ma kintsamana komai.

DA darema hajiya zagewa tai wajan kuma nunamin yanda Zan gyara kaina taitayi da sauran dubarun zaman aure tunda yanzu nadan kuma hankali ba kamar farkoba.

""**""

"Yauwa Sadiq zo ka idasa goge wajannan inje inyo aski indawo"Cewar daddy wa inda ketafaman gyare gida duk sabida dawowarmu.
Dariya Sadiq din yasaki kamin yace to"Ai daddy kajira mu idasa saimutafi tare muma munaso muyi askin ai yanda zata gammu fes.

Hararar wasa daddyn ya sakarmishi kamin yace "Wato sabida kaga ka kusa taddoni tsawo shine kakeneman rainani ko? To karma kafara nikadai zanje Allah.
Yana niyyar fitane Saiga zahra da uban cikinta agaba kafafu duk sun kumbure,Kallon mamaki daddy yabisu dashi musamman ya usi dake rike da Jakarta Ahannu.
"Kai bansan hauka daga Ina zuwa Ina haka?

Dan sosa kai ya usin yayi kamin yace"Daddy anwuni lafiya?
Hararashi dadyn yayi kamin yace bakaji tambayar danayiba kenan?

"Uhum daddy dama daga gida muke kuma iyakarta nan Sabida zata taryi jiddane kuma dama asbt ance tadan dinga tattaki shine na rakota anjima sai indawo daukarta.

Haba dadyn yakama kamin yace,Ammadai yakamata kurage yawo kaga DA ga yanzu zuwa kowane lokaci zata iya haihuwa Dan haka ku kiyaye indai ba so kukeyi ahaihu ahanya ba,Ficewa yayi bedaina fadaba.

Saida ya temakamata Sannan ta zauna gidan ko Ina tas yashagyra ga kulolin abinci Wanda hajiyakaka ta aiko dasu sabida tarar baki.
"Sadiq Ina daddy zashine naga kamar sauri yakeyi?

Saida yai dariya Sannan yace ba sauri yakeba wallahi aski zashi tun jiya yake kalkale kalkale saikace mace inaga duk gyaran tarar aunty ne.

Bugu ya usin yakaimishi duk suna dariya,Saida yahuta Sannan yabar gidan da niyyar insha Allah zaizo ya maidata gida dawuri basaidare yayiba.

***

Alhamdulillah yaudai gashi nadawo gidan mijina kuma Nagode Allah domin nasami tarba ta musamman daga matan yayun daddy dakuma Hajiya kaka gakuma aminiya zahra da k'aton cikinta😅.

Sai daf DA magriba Sannan akawatse gidan yakoma daga mu Saimu,Dabhaka nabawa Mimi haidar mukafara gyaran gidan yaudai hadda daddy aikin.

74-5

Komai da walwala da farinciki mukeyinshi Dan gaskiya munyi missing din juna, Saida haidar yafara kuka Sannan daddy ya karbeshi mukuma mukaci gaba da aikin,Saiwajan goma saura Sannan muka kintsa ko'ina tuni faruk da Mimi sunyi barci tunda angaji.

Saida na shiryar haidar haryai barci Sannan nima nashiga wanka lokacin daddy yai wani dai-dai akan gado da alama jirana yakeyi.

Humrata me matukar kamshi nashafa jikina tare da saka rigar barci'yar Mara nauyj tunda naji garin akwai zafi babu laifi.

Saida nagama kalkalena Sannan na raba gefenshi na kwanta.

Rungumeni yayi cikin jikinshi yana Sauke ajiyar zuciya Dan wata irin nutsuwa yakejin tana sakkowa cikin jikinshi.

Cikin wata sassanyar murya ya furta"Nai kewarki sosai Jidda'Ina matukar bukatar kasancewa dake saidai naga kingaji dayawa yau.

Kuma shigewa nai jikinshi inajin yanda tausayinshi kekuma dannemin zuciya"Karka damu daddynmu Zan iya ai dannima nai kewarka irin sosai dinnan.

Dan murmushi yasaki kamin yafara gwadamin zazzafar kaunarshi Dan daddy akwai zafin hannu.

Basainace ga yanda akaiba Amma nasan kowa zai hasaso wannan dare,Alhamdulillah Lafiya qalau natashi sai gajiya data rafkeni to ko daddyn saida jikinshi yai laushi balle kuma ni.

Allah ya temakeni haidar bed a yawan fitina shiyasa nai kwanciyata bayan Sallar asuba.

Saidai me daddy nadawo masallaci yafara neman k'ari.

Manyan idanuna na zubemishi yayinda cikin zuciyata nake mamakin wai duk irin yin da yayi jiya Amma yanzuma k'arawa zaiyi toma abinda suke fitarwa be k'arewa ne.

"Dan marairaicewa nayi Ina kallonshi danyaji tausayina Dan sosai nasha wahala jiya Dan ba k'aramin gyara nashaba wajan Hajiya,Shima marairaicewar yayi hadda langabe kanshi gefe guda kamin yace"Pls jiddana ko kadanne kinji!!

Kusan saida gari ya idasa wayewa Sannan ya barni lokacin ko hannuna sainayi da gaske nake motsashi Sabida gajiya,Shi kanshi uban gayyar tunda ya kwanta yake maida numfashi Amma banji yai motsin kirkiba,Bayan rungumata dayai.

Allah ya rufamin asiri yau lahadi nasan da anji babu dadi.

Haidar ne ya tashi, Danhaka na lallaba nawuce toilet dan gyara jikina,Shikuma daddy ya dauki yaron yana jijjigashi.

Yaudai bamu karya da wuriba tunda an makara,Amma yaran babu wanda yasamu musamman da ganin haidar ya daukemusu hankali Sai wasa sukemishi.

Bayan sati daya; Cikin kwanakinnan ba karamar jigatuwa nakeba hannun daddy Sam babu sauki duk inda naso zanzarewa yananan like ko damuwa da yaranshi zasugane meyakeyi beyi,Yayinda na canza idanuna sundan fada Ammafa nai kyau jikina yakuma murjewa daka ganni kasan Ina cikin nutsuwa da kwanciyar hankali.
Amma bangaren daddy ai sai Sam barka Dan tuni yai kiba ya canza koda yaushe cikin frinciki yake da walwala.

***

Yaudai gabadayanmu gidan zahra muka nufa yau, Daddy ya ajemu bayan yagama jiddadamin da anyi la'asar mukoma gida koda bezoba.

Cikin farinciki zahra ta tarbemu duk dacewa zaune take sabida yanda cikin yaimata wani girma gabadayama ta kumbure cikin kanshi zaune yake akan cinyiyinta"Ikon Allah wai zahra haka cikinnan Ya maidaki Sannu inagadai biyune gaskiya.

Dan hararata tayi kamin tace" A a kin manta uku ne.

Banwani zaunaba sabida yanda gidan Nata yake babu kintsi nasan nauyin DA tayine yasata kasa gyaran,Shiko dama gyaran namiji ba lallai yai kamar na maceba.

Har girki Saida naimana domin ya usi na shigowa yai farinciki daganina kamin yace"Yauwa yau munhuta da shan tea da rana do min dahuwar tea kawai ya iya hadawa saikuma farar shinkafa.

Hira mukeyi cikin farinciki da walwala"Nagode Jidda nagode sosai Allah ya sakamiki da alkhairi Allah ya jikan iyayenmu.

Tare muka amsa da amin kamin inbita da kallon dalilin godiyar.

"Dole naimiki godiya jidda kin kawo farinciki me tarin yawa cikin gidanmu,Daddy ya canza canjin da kowa ke magana kuma kalli wa innan yaran ma basu taba kawomin wani korafi akan kiba,Hakika YARDAr danaimiki bata tashi abanzaba,Shiyasa nakekumajin alfahari dake Jidda nagode sosai, Wallahi ko yanzu Allah ya dauki rayuwata nasan banda damuwa akan kannena

domin alhamdulillah daddy yayi dace da mata'Mata irin ta nunawa sa'a fatana Allah yasa ki dore ahakan nagode.

Jikina naji yaiwani irin Sanyi nan da nan idanuna suka ciko DA kwalla dan tunanin mutuwane kawai ya darsu cikin raina.

Hannuwanta na rike Ina kallon cikin idanunta,Zahra kindaisan ba'ason meciki da shiga damuwa ko? To Dan Allah ki kwantar da hankalinki Lafiya lau zaki haihu mu rayu tare zakiga abinda zaki Haifa kamar yadda nakeganin nawa, kuma zamu kasance tare insha Allah.

Hannuwana ta matse cikin nata tana murmushi"To shikenan nagode sosai,Yakamata kitashi kuje gidafa kinga har yamma tayi kadda daddy yai fada nima gobe zamu koma ganin likita dama sati daya sukabada idan ban haihuba to kinga shiru kuma ga ciwo inaji.

"Eh gara ku komadin Allah ya raba lafiya,Kai Sadiq jeka taromana me napep muwace kadda musha fada.

Nidai koda mukabaro gidan hankalina dukba kwanceba,Sabida gaskiya kallo daya zakaima zahran kasan tanashan wahalar cikin.

Cikin dare.

Kuma shigewa nai jikin daddy Wanda yaketa sauke numfashin samun nutsuwa Dan yanzu yagama cakudani.

Mannamin kiss yayi saman goshina kamin yace"Nagode jiddana me kikeso naga kina ta motsi ko in tausamiki jikinki ne?

"A a daddy kawaidai hankalina yaki kwanciya zahra batajin dadin jikinta wlh kuma duk ta canza dazuma duk ta kumbure.

Kaina yake shafa ahankali cikin nutsuwa kamin yace "Karki damu dama lalurar ciki yawane da ita,Amma insha Allah zata haihu Lafiya saidai mutayata da addua,Tashi muje ki gyara jikinki.

** ** **

Tun Ina sallar asuba ake kiran wayar daddy danhaka saida nagama Sallar sannan na dauki wayar saidai tuni kiran ya yanke,Ina ajiye wayar Saigashi wani kiran yashigo ta wayata.

Wani irin mummunan faduwan gabane ya sameni kamin indauki wayar da sauri.

"Ya usi"

"Na'am jidda Ina daddy inata kiran wayarshi be daukaba Dan Allah kimishi magana.

Agaggauce nace masallaci yaje be dawoba tukunna lafiya?

Aika ko Mimi ne ta kirashi zahrace ta haihu yanzu yara biyu mace da namiji Amma kuma bata motsi bazan iya kaita asbt ba kuma bansan Wanda Zan nemaba yanzu.

Hijab dina na yayiba tuni nafara kuka, Ahanya mukai Karo dashi,Arude yake tambaya lafiya?
Bayani naimishi inayi Ina kuka.

Shima nan hankalinshi yatashi Ya dauki mota ko haidar bamufita dashiba.

Saida mukabiya muka dauki wata abokiyar aikinshi mace Sannan muka isa gidan.

Tashin hankali,Ya usi zaune da yaran rungume sunata tsala ihu shima yana tayasu gakuma zahra kwance babu numfashi jikinta.

End.

Basainace hankula suntashiba domin zai iyazama bata lokaci,Shi kanshi daddyn wani irin zaman dirshan yayi yana sauke numfashi,Yayinda zuciyarshi tafara tunamishi da rashin da yayi awancan lokacin.
Dr.hajara itace tai karfin halin fara duba zahra din aiko saita fahimci bawai mutuwa tayiba tsabar wahala yasata doguwar suma.

"Dr.kuje asbt tanada rai bari in shirya yaran saimu biyoku daga baya nida madam.
Zumbur duk suka mike daddy da ya usin,shine ya dauketa suka fice kowa jiki na rawa.
Daddyne yai tukin danyafishi dan nutsuwa ba laifi.

Nidai iyakacina riko,Ina kallon matarnan ta gyare yaran tsaf,Sannan ta gyare wajan nikuma yaran na hannuna Ina jijjiga Dan sosai suke ihun kuka da wutsul wutsul.

Saida komai yai daidai sannan muka fice gidan Allah yasa key din motar ya usi na kusa.

Alhamdulillah tunda sukaje komai Lafiya qalau domin anyimata duk temakon daya dace lokacin gari ya waye ma.

Gabadayanmu zaune muke munyi jigun jigun Dan har lokacin bata farkoba,Ga yaran sai kuka sukeyi,Ni Kai na nonona yaimin hake hake to haidar na gida.

Mikewa daddyn yayi ya kallemu"Bari inje Gida wajan yarannan bamusan halin da suke cikiba Sannan nasan kila haidar nacan na kuka dan rabonshi da abincinshi tun dare.

Duk DA to muka amsa Sannan yafice danyasan alokacin kodayace ni inje gidan bawai zuwa zanyiba,Kuma har lokacin bamuyi tunanin mugayama wasuba.

Yai mamaki lokacinda yashiga gidan ko Ina tsaf yanata tashin kamshi,Gakuma faruk DA Mimi sunashan tea da kwai,Ga Sadiq tsaye yana jijjigar haidar Wanda keta korafi.
Ajiyar zuciya ya sauke kamin ya furta*Alhamdulillah abayyane yana karasowa Cikin falon.

Gaidashi sukai,Sannan ya amshi haidar din daketa rarume-rarumen nono DA alama yunwa yakeji sosai.

Zamayai sannan yagayamusu abinda yafaru ya Dora dafadin rikeshi inwatso ruwa Sadiq sai inzo inkainatashi Dan da alama ta manta dashi ma.

Bayan tafiyar daddy Zahra ta farko kuma Alhamdulillah qalau tatashi danhaka dagani har ya Usi din baki har kunne.

Gaskiya zahra ta jigata,Munanan munata murna saiga daddy dakuma yaran gabadaya,Wayyo sai lokacin naji tausayin yarona musamman daya cafki nonon har kwarewa yakeyi.
Idanu daddy ya zubamin nasan korafi yakeso yayi, aiko muna hada ido na turo bakina gaba Dan karma yace wani abu,Murmushi kawai yayi tare da kauda kanshi.

Su hajiyama kusan tare suka shigo,Daganan kuma kamin wani lokaci wajan yacika tuni ya usi da daddy sukabar wajan duk DA akwai yiwuwar zuwa dare mukoma Gida.

***

Alhamdulillah komai yayi yanda akeso kuma ake bukata.
Yara sunci sunan mamanmu da abbanmu inda ake sakaya sunan da SULTAN DA SULTANA. Yarane masu matukar kyau dashiga rai,Zahra ta warware Dan tuni tadawo hayyacinta yanzukuma sai kula da yara.

""**""

Bayan shekara biyar:
Kwance nake ina kallon Mimi da kannenta har uku wasa sukeyi sai ihunsu kawai dayacika gidan Dan kowanne beji indai wajan rashin jine.
Bayan haihuwar Haidar da wata shadaya nakuma samun ciki Wanda saida mukakai ruwa rana da daddy akanshi Amma Allah yayi saida na haifeshi inda yaci sunan Ahmad,Naso kwarai inyi planing alokacin Amma yaki yarda aiko saigashi Ahmad na shekara daya nakuma samun wani cikin,Alokacin haukane kawai banyiba Amma har yaji saidanayi gidan hajiya Amma abanza Dan saida na haifi Usman cikin ikon Allah kuma saigashi yanxu Ina hutawa duk dacewa kusan atsorace nake Amma har yanzu bansami cikinba.
Abangaren zahra ko yaro daya takuma haihuwa bayan twins dinta inda yaron yaci sunan daddy amma ana kiranshi da khalifa.
Bazancrmuku ga ranar datazo muka sami sabani da zahraba kuma kusan duk weekend takanyi kokarin yinshi wajena,Kaunar da takemin nasan batakai wadda nakemataba duk da cewa inajinta araina fiye da kowa yanzu.

Maganar makaranta kuwa tuni karatunmu ya mika domin dafarko daddy kin yadda yayi Amma dagabaya ranakwatsam yace inshirya zamufita,Ban tambayeshiba kamar yadda nasaba nasako hijab dina,To dama yanzu bawai fita da yaro nakeba tunkan haidar sabida ga 'yan uwanshi gidan matukar basuje makarantaba.
Daganan nakoma karatuna wanda gashi yanzu ina daf da zama ma'aikaciyar jinya.

Tsakanina da daddy sai Sam barka domin nidai har yanzu bazan iya bugun kirji infadi wani kwakwkwaran laifinshiba kullun kokarin kyautatamun yakeyi haka yaranshi biyayyar da sukemin koni na haifesu iyakarta kenan,Shiyasa gaskiya ni bazan boyeba auran babban mutun yaimin Rana domin nasan da wuya insami hakan daga saurayi metashen samartakarshi,Waima kunsan cewa duk inyana gida tare mukeyin komai dashi? Kuma yanzu haka duk lokacinda yake gida wankana nashine haka shafa aikina kawai kwalliya itama danyace be iyaba.
Idan kukaji yanda muke hira ake arerewa dashi saikuyi mamaki.
Bazangaji da godema Allah ba akan wannan baiwa dayaiminba.
Gabadaya yanzu inada shekara aShirin da daya kusan Zan iyacewa sai yanzune nakekan ganiyar girmana nai wani irin kyau da tsari,Shiyasa yanzune daddy yafi nuna kishinshi zallah akaina be yarda inje konan dacan batare dashiba,Daidai da Media be yarda inyi hulda da kowaba.
Alhamdulillah kamar yadda bani da matsala hakama ta bangaren zahra,Lokuta da dama

mukan bawa junanmu shawarwarin dasuka dace batare da manyanmu sunjiba,Tabbas na YARDA da cewa YARDA tanasa komai arayuwa tunda gashi mudai YARDA ce ta kasance jigo akan komai namu.

***

Zaune nake cikin falona chatting nakeyi da zahra sai kwasar dariya nakeyi gidan ni kadaice domin tun safe sukatafi gidan Hajiya kaka shiyasa nake hankalina kwance.

Sallamar daddy yasani yimata sallama Sannan na ajiye wayar tare da mikewa,Sannu da zuwa daddy"

"Yauwa madam ya gidan anbarki ke kadai ko? Ya idasa maganar yana shigardani jikinshi.

Saida na juya idanuna yanda nasan zaiji ajikinshi Sannan nace"Eh Amma Lafiya lau Dan naji sakat yau kunnena ya huta.

Dariya yasaki kamin yace"Ainaga alama tunda gakinan kinata hira abinki yakamata kizo inkara yimiki wata kyautar DA izinin Allah Dan gaskiya zamanki ya isa hakanan.

Manyan idanuna na zubamishi da alamar tsoro kamin ince"Kai daddy Dan Allah kayi hakuri wallahi ban hutaba dukafa ko shekara daya da rabi be idasaba Dan Allah karkamin.

Rukomin kugu yayi yana shafar mazaunaina"Karma kifara wallahi nafison infingajin hayaniya koda yaushe cikin gidannan Dan gaskiya hakan shine burina.

Turo bakina gaba nayi tare da kwace jikina,Nidai gaskiya ban yardaba wallahi tunda bakasan wahalar da nakeshaba wajan haihuwar dole kaita kiramin ita.

Rikoni yayi ya na dariya" Kedai anyi raguwa wallahi laulayin da rainon ai duk Ina tayaki haihuwarce kawai kikeyi ke kadai to nidai gaskiya inason sabon baby.

Duk tirjiyata bata hanashi kaini gadonshiba kuma nan da nan yaimin runfa DA faffadan kirjinshi,Kamin wani lokaci na manta inda kaina yake.

Sai bayan da komai ya lafa sannan nafara kumbure-kumbure Shikuma ya shigar dani jikinshi yana dariya,Tare da tsokanata Allah yasa biyu sunshiga.

ALHAMDULILLAH DUKA ANAN NAKAWO KARSHEN WANNAN LABARI MESUNA YARDA.Inafatan Allah ya gafartamin kuren dake cikinshi.

Masoya labarin YARDA nagode sosai da daurema bibiyar labarin da kukai Allah yabar zumunci tsakaninmu nagode.

Taku har kullun MAMAN KHADIJA.

Saimun hadu asabon littafina insha Allah mesuna FATIMA saidai shi zaizomukune gabadayanshi insha Allah Dan haka babu maganar zaman jira cikin labarin FATIMA.

NAGODE.